# Gado ƙarfin Allah

# La force du lait

Daga / de Yazi Dogo

Mai fasarawa/Traductrice : Saoudé Elh Salifou

**Taƙaitawa :**

Wani sarki ne da zai mutu ya tattara fadawa ya ba su amanar ɗansa akan su naɗa shi bayan mutuwarsa. Amman bayan mutuwar sa sai suka ƙi cika alkawali.
A zamanin da, in sarki ya rasu fadawa da bayin sarki suke taruwa su naɗa sabon sarki cikin mainawa. Kafin lokacin zaɓe kowane maina sai ya aje takardarsa ta neman takara kuma sai ya fara parpagandi. To nan ne kai maina in kana da kirki za ka gani in kuma baka da kirki sai ka gani.Bayan haka nan kuma wasu sai su shiga neman malammai da bokaye. Ranar zaɓe mainawa sun zo sun jera suna tsammanin za a yin irin na galgajiya. Amma zamani ya canza yanzu gwamnati da parti su suke zaɓar wanda suke so a kan dalilan siyasa.
Furefe ya zo da takardarsa mai ɗauke da sunnan wanda gwamnati ya zaɓa. Sauran mainawa suka so su gama kai don su cutar da sabon sarkin. Amma sai shi sarkin ya neme su don su haɗa kai su yi wa ƙasarsu aiki tare, ya ba kowane daga cikin su muƙami.

**Résumé :**

C'est l'histoire d'un roi qui, avant de mourir, fait venir ses notables pour leur confier son enfant afin qu'il soit élu après sa mort. Mais après sa mort, les notables n'ont pas tenu parole. Traditionnellement après la mort d'un roi, les notables et les serviteurs se réunissent pour élire le nouveau roi parmi les princes. Avant les élections chaque prince doit déposer sa candidature et commencer sa campagne. C'est le moment pour les princes de mesurer leur popularité.
Dès lors, certains prétendants vont consulter marabouts et charlantans. Le jour venu, les princes se présentent tous, pensant que la tradition sera respectée. Mais les temps ont changé, maintenant c'est le gouvernement et le parti qui choisissent qui ils veulent parmi les héritiers sur des considérations politiques.
Le préfet vient alors avec le décret portant le nom de celui que le gouvernement a choisi. Après l'intronisation les candidats malheureux se sont réunis pour contester l'élection du nouveau roi. Mais celui-ci les rassembla, les exhorta à se joindre à lui dans l'intérêt de leur pays et attribua  à chacun une fonction de dignitaire à la cour.-

**Gado ƙarhin Allah**

**<u>TABLEAU I</u>**

*Sarki a cikin ɗakinsa kwance yana jinya. Wani bafade mai suna Kalla yana gyaggyara shi tare da yi masa fita. Wani dogari, mai suna Jirɗi yana tsaye bakin ƙofa da sanda riƙe a hannunsa.*

*Le roi dans sa chambre, très malade. Deux notables sont avec lui. L'un du nom de Kalla le met dans une position confortable et le deuxième Jirdi est devant la porte tenant son bâton.*

Sarki: Kalla!

Le roi : Kalla!

Kalla: Allah ya baka nasara!

Kalla : Votre Majesté !

Sarki: Kalla a kira min limam.

Le roi : Kalla, appelle-moi l'imam.

Kalla: Jirɗi!

Kalla : Jirdi !

Jirɗi: Ranka ya daɗe!

Jirdi : Votre Majesté !

Kalla: Ka yi maza ka kira limam. Ka ce kuma sarki na kira.

Kalla : Appelle vite l'imam. Dis lui que le roi veut le voir.

Jirɗi: Insha Allahu!

Jirdi : Par la volonté de Dieu !

Kalla: Maza! E, maza!

Kalla : Fais vite !

*Jirɗi ya fita da sauri zuwa kiran limam. Jim kaɗan ya dawo. Har yanzu sarki yana kwance ciwo ya dame sa.*

*Jirdi se précipite dehors pour appeler l'imam.  Après un moment il revient et trouve le roi toujours couché, agonisant.*

Jirɗi: Ranka ya daɗe, yana zuwa.

Jirdi : Votre majesté, il arrive.

Kalla: Ka same shi ko?

Kalla : Tu l'as trouvé, n'est-ce pas ?

Jirɗi: E! Na same shi, nan wajen bakin masallaci.

Jirdi : Oui ! Je l'ai trouvé à côté de la mosquée.

Kalla: To madalla!

Kalla : Bien !

Sarki *(Yana shaƙƙuwa)* : Kalla!

Le roi *(En hoquettant) :* Kalla !

Kalla: Allah baka nasara!

Kalla : Votre Majesté !

Sarki: Gyara mani hannuna

Le roi : Ajuste-moi mon bras.

Limam *(Ya shigo):* Salama alaikum!

L'imam *(S'annonçant) :* Que la paix soit avec vous.

Kalla da Jirɗi: Alaika salam!

Kalla et Jirdi : Que la paix soit avec vous aussi !

Kalla: Gafarta malam!

Kalla : Béni soit malam !

Jirɗi: Gafarta malam!

Jirdi : Béni soit malam !

Kalla: Allah baka nasara, malam kin ne.

Kalla : Votre Majesté, malam est là.

Sarki : Tau.

Le roi : D'accord.

Limam *(Ya yi fatiya)* : Bismillahi Rahamani Rahim. Alhamdu lillahi Rabil alamina. Arahamanir Rahim Maliki yau midin. Fatiya!

L'imam *(Récite une prière)* : Bismillahi Rahamani Rahim. Alhamdu lillahi Rabil alamina Arahamanir Rahim Maliki yau midin. Amen !

Kalla: Amin!

Kalla : Amen !

Limam: Kalla!

L'imam : Kalla !

Kalla: Gafarta Malam!

Kalla : Oui, votre Eminence !

Limam: Yaya mai jiki?

L'imam : Comment va le malade ?

Kalla: Alhamdu lillahi!

Kalla : Dieu merci !

Limam: Yaya? Ya sha wani abu ma?

L'imam : Alors, a-t-ilpu boire quelque chose ?

Kalla: A'a!

Kalla : Non !

Limam: Bai sha hwarau-hwarau ba?

L'imam : N'a-t-il pas bu du foura dilué ?

Kalla: A'a, tun jiya.

Kalla : Non, Il n'en a pas bu dépuis hier.

Limam: Tun jiya! Kwana uku mutum bai sha hwarau-hwarau ba, ina mutum. Allon ƙarhen da na aiko an wanke an bashi?

L'imam : Quoi ! Il n'a rien bu dépuis trois jours, ce n'est pas normal ça. A-t-il bu l'eau bénite lavée de la tablette métallique que j'aie envoyée ?

Kalla**:** E! Tsaya dai in tambayi Jakadiya. Jakadiya!

Kalla : Oui ! Mais je vais encore demander à la dame de la cour.

Jakadiya: Na'am!

Jakadiya : Oui !

Kalla: Allon nan an wanke, na ƙarhen da limam ya aiko?

Kalla : la tablette métallique que l'imam a envoyée a-t-elle été lavée?

*Jakadiya ta shigo da kwano mai ruwan rubutu ta miƙa ma Kalla.*

*Jakadiya rentre avec sa tasse contenant l'eau bénite et la donne à Kalla.*

Kalla: A, shi ne?

Kalla : Ah, c'est ça ?

Jakadiya: Shi ne, an wanke.

Jakadiya : C'est ça, c'est lavé.

Kalla: Tau!

Jakadiya : D'accord !

Limam: A kawo hura.

L'imam : Amener du foura.

Kalla: A kawo hwarau-hwarau kuma.

Kalla : Apporter le foura dilué.

Limam: Ba shi ya sha. Ina? Mutum kwana uku bai sha hura ba, ina mutum? Tada shi Kalla

L'imam : Donne lui à boire. Non? Pendant trois jours, il reste sans rien manger ? Kalla aide-le à se lever.

Kalla: Allah baka nasara! Allah baka nasara!

Kalla : Votre Eminence ! Votre Eminence !

Limam: Tada shi Kalla, Tada shi!

L'imam : Aide-le à se lever Kalla. Aide-le.

*Kalla ya tallaba sarki ya tashi zamne.*

*Le roi se met assis avec l'aide de Kalla.*

Limam: Allah baka nasara ba dađi ba ke dakwai, sha dai za a yi haka. Hura ce.

L'imam : Sa Majesté c'est difficile, mais tu vas essayer de boire. C'est du foura.

Kalla: Ba ya sha ba.

Kalla : Il ne va pas boire.

Limam: Bai ya sha?

L'imam : Il ne boit pas ?

Kalla: Haka nike wannan hwaman kullun.

Kalla : C'est comme ça que je lutte chaque jour.

Limam: Bari a ba shi rubutu.

L'imam : Laisse on va lui faire boire l'eau bénite.

Kalla: I, yo kuma?

Kalla : Ah, bon ?

Limam: Rubutu ne.

L'imam : C'est l'eau bénite.

Sarki**:** Tau!

Le roi : D'accord !

*Limam da Kalla sun tada sarki daga kwance suka ba shi rubutu ya sha. Sa'annan limam ya shafa masa ga fuska, hannu da ƙafafu.*

*L'imam et Kalla aident le roi à s'assoir et lui ont donné l'eau bénite. Ensuite l'imam lui a passé l'eau sur le visage, les mains et les pieds.*

Sarki: Kalla!

Le roi : Kalla !

Kalla: Allah baka nasara!

Kalla : Votre Majesté !

Sarki: Kwantan ni.

Le roi : Aide-moi à me coucher.

Limam: Kwantan shi.

L'imam : Aide-le à se coucher.

Sarki: Kwatan ni.

Le roi : Aide-moi à me coucher.

Limam: Kwantan shi.

L'imam : Aide-le à se coucher.

*Limam ya tashi ya tofa wa sarki addu'a a jikinsa, Kalla ya gyara masa kwanci ya yi masa fita kuma ya ƙara rufe shi.*

*L'imam fait des invocations au roi et Kalla l'aide à se coucher et le couvre d'un vêtement.*

Limam: Bari a mai adda'a, a mai waƙataƙulahu ƙafa gomiya tara a gani.

L'imam : Je vais lui faire des invocations pour voir.

Sarki: Kalla!

Le roi : Kalla !

Kalla: Allah baka nasara!

Kalla : Votre Majesté !

Sarki: A kira min hwadawa.

Le roi : Appellez moi les notables.

Kalla: Jirɗi!

Kalla : Jirdi !

Jirɗi: Allah baka nasara!

Jirdi : Votre Majesté !

Kalla: Tahi nan bakin ƙofa, duk mayan, mayan nan, su Galadima, su Ciroma…

Kalla : Va à l'entrée, appelle les grands notables, Galadima, Tchiroma…

Jirɗi: Insha Allahu!

Jirdi : Si Dieu le veut bien !

Kalla: Su waziri, du su shigo.

Kalla : Les waziri dis leur de rentrer.

Jirɗi: Insha Allahu! Insha Allahu!

Jirdi : Si Dieu le veut bien ! Si Dieu le veut bien !

Kalla: E, mayan mayan su shigo.

Kalla : Oui, qu'ils rentrent.

Jirɗi: Insha Allahu!

Jirdi : Si Dieu le veut bien !

Kalla: Yi maza!

Kalla : Fais vite !

*Jirɗi ya fita kiran fadawa. A kofar fada akwai fadawa biyu tsaye a kowane ɓangaren ƙofar.*

*Jirɗi ya dawo da gudu.*

*Jirdi sort pour appeller les notables. A la porte se trouvent deux notables, un de chaque coté.*

*Jirdi revient en courant.*

Jirɗi *(Ya durƙusa)*: Allah ya baka nasara, suna zuwa.

Jirdi *(S'accroupi) :* Votre Majesté, ils arrivent.

Kalla: Ka same su?

Kalla : Tu les as trouvés ?

Jirɗi: E, du na same su gaba ɗaya.

Jirdi : Oui, ils sont tous là.

Kalla: Tau madalla!

Kalla : Merci !

Jirɗi: E!

Jirdi : Oui!

Sarki: Kalla!

Le roi : Kalla !

Kalla: Allah baka nasara!

Kalla : Votre Majesté !

Sarki: Gyara min wannan hannun nawa.

Le roi : Arrange-moi cette main !

Kalla:Tau!

Kalla : D’accord !

*Fadawa sun shigo cikin ɗakin sarki inda yake kwance kowa ya samu wuri ya zamna.*

*Les notable sentrent dans la chambre où se trouve le roi et prennent place.*

Fadawa: Allah ya baka nasara!

Les notables : Gloire à toi !

Limam, Kalla da Jirɗi: Amin! Amin! Summa amin! Amin!

L’imam, Kalla et Jirdi : Amen ! Amen ! Encore amen ! Amen !

Waziri: Allah baka nasara!

Waziri : Gloire à toi !

Limam, Kalla da Jirɗi: Amin waziri!

L’imam, Kalla et Jirdi : Amen waziri !

Galadima: Allah baka nasara!

Galadima : Gloire à toi !

Limam, Kalla da Jirɗi: Amin Galadima!

L’imam, Kalla et Jirdi : Amen Galadima !

Ciroma: Allah baka nasara!

Tchiroma : Gloire à toi !

Limam, Kalla da Jirɗi: Amin!

Limam, Kalla et Jirdi: Amen **!**

Kalla: Allah baka nasara, ga su Waziri nan.

Kalla : Votre Majesté les waziri sont là.

Sarki: Sun zo?

Le roi : Ils sont là ?

Kalla: E, ga su sun zo.

Kalla : Oui, Ils sont là.

Sarki: To, tasan ni.

Le roi : Bon, aide-moi à me lever.

Fadawa: To, yaya aka ji da jiki?

Les notables : Comment va le malade ?

Limam, Kalla da Jirɗi: A, Alhamdu Lillilahi! Alhamdu Lillilahi!

L’imam, Kalla et Jirɗi : Dieu merci ! Dieu merci !

Fadawa: Allah ƙara sauƙi.

Les notables : Que Dieu lui accorde la santé.

Limam, Kalla da Jirɗi: Amin, amin, amin summa amin!

L'imam, Kalla et Jirɗi : Amen, amen, amen encore amen !

Sarki: To, Galadima!

Le roi : Eh bien, Galadima !

Galadima: Allah baka nasara!

Galadima : Votre Majesté !

Sarki: Ciroma!

Le roi : Tchiroma !

Ciroma: Allah baka nasara!

Tchiroma : Votre Majesté !

Sarki: Ina Waziri?

Le roi : Où est Waziri ?

Waziri: Allah baka nasara!

Waziri : Votre Majesté!

Sarki: Kun zo ku? Yauwa!

Le roi : Vous êtes là ? Bien !

Fadawa: E!

Les notables : Oui !

Sarki: Ina Ɓaidu?

Le roi : Où est Baidou ?

Kalla: Jirɗi!

Kalla : Jirdi !

Jirɗi: Allah baka nasara!

Jirdi : Gloire à toi !

Kalla: Tafi nan gidan Magaram maza ka ce Ɓaidu ya zo ana kira.

Kalla : Va chercher Baidou chez Magarame, dis lui de venir vite.

Jirɗi: Insha Allahu! Tau!

Jirdi : Si Dieu le veut bien. D' accord !

Limam: E, na gan shi, yanzu ya shiga.

L’imam : Oui, je l’ai vu, il vient juste de rentrer.

Jirɗi *(Ya fita zuwa kira Ɓaidu):* Tau, tau!

Jirdi *(Part chercher Baidou) :* D’accord ! D’accord !

Fadawa *(Sarki yana tari yana shaƙƙuwa):* Asha! Asha! Allah ya koro sauƙi, Allah ya koro sauƙi!

Les notables *(Le roi très souffrant) :* Désolé ! Désolé ! Que Dieu t’accorde la santé ! Que Dieu t’accorde la santé !

Limam da Kalla: Amin! Amin!

L’imam et Kalla : Amen ! Amen !

Jirɗi: Allah baka nasara, na same shi,

Jirdi : Votre Majesté, je l’ai vu.

Kalla: Ka same shi?

Kalla : Tu l’as vu ?

Jirɗi: E! Na same shi, nan ma muka gamu kan hanya. E!

Jirdi : Oui, je l’ai vu, nous nous sommes rencontrés en cour de route. Oui !

Fadawa: Yana nan ko?

Les notables : Il est là ?

Jirɗi: E, yana nan.

Jirdi : Oui, il est là.

Kalla: To!

Kalla : D’accord !

Ɓaidu *(Ya shigo cikin falon sarki):* Salama alaikum!

Baidou *(Entre dans le salon du roi) :* Que la paix soit avec vous !

Fadawa: Zamna nan, zamna nan

Les notables : Prends place ! Prends place !

Ɓaidu: Allah baka nasara!

Baidou : Gloire à toi !

Fadawa: Amin Ɓaidu, amin Ɓaidu!

Les notables : Amen Baidou, amen Baidou !

Sarki: To, hwadawa!

Le roi : Eh bien, les notables !

Fadawa: Allah baka nasara! Allah ya taimake ka!

Les notables : Votre Majesté ! Que Dieu vous aide !

Sarki: Kuna jin abin da zan gaya maku?

Le roi : Vous m'écoutez ?

Fadawa: Allah baka nasara!

Les notables : Gloire à toi !

Sarki: Ba yau ba muke tare da ku.

Le roi : Ça fait longtemps que nous sommes ensemble.

Fadawa: Gaskiya ne, Allah ba ka nasara!

Les notables : C'est la vérité, votre Majesté !

Sarki: Shekara talatin da biyar muke tare da ku.

Le roi : Ça fait trente cinq ans que nous sommes ensemble.

Fadawa: Gaskiya ne, gaskiya ne, Allah baka nasara.

Les notables : C'est la vérité, c'est la vérité, votre Majedté.

Sarki: An na saɓa maku, ku yafe mini.

Le roi : Si je vous ai fait du tort, pardonnez-moi.

Fadawa: Assha! Assha! Allah baka nasara.

Les notables : Désolés ! Désolé ! Votre Majedté.

Sarki: Wannan cuta ba bari na ba za ta yi.

Le roi : Cette maladie me sera fatale.

Fadawa: Assha! Assha! Allah baka nasara!

Les notables : Désolés ! Désolé !  Votre Majedté !

Sarki: Wannan cutal ba bari na ba za ta yi.

Le roi : Cette maladie me sera fatale.

Fadawa: Assha! Assha!

Les notables : Désolés ! Désolé !

Sarki: To ga Ɓaidu!

Le roi : Bon, voilà Baidou !

Fadawa: Um!

Les notables : Oui !

Sarki: Na ba ku amana.

Le roi : Je vous le confie.

Fadawa: Um!

Les notables : Oui !

Sarki: A riƙi amana, na ba ku amana.

Le roi : Je vous le confie.

Fadawa: Amana mun riƙe, Amana mun riƙe hal lahira.

Les notables : Nous prennons l'engagement jusquà la mort.

Sarki: Limam na ba ku amana, a riƙi amana, na ba ku amana ɗana Ɓaidu. A riƙi amana. E, a riƙi amana.

Le roi : L'imam je vous le confie, il faut tenir parole, je vous confie mon fils Baidou. Il faut tenir parole. Oui, il faut tenir parole.

Fadawa: Ba komi, cuta ba mutuwa ba ce.

Les notables : Ça ne fait rien, c'est la maladie ce n'est pas la mort.

Sarki: Kalla!

Le roi : Kalla !

Kalla: Allah baka nasara!

Kalla : Votre Majesté !

Sarki: Kwantan ni.

Le roi : Aide-moi à me coucher.

Fadawa: Za mu fita daga fada, Allah koro sauƙi.

Les notables : Nous allons nous retirer, que Dieu vous accorde la santé.

Kalla da limam: To amin, amin!

Kalla et limam : Amen, amen !

*Fadawa da limam suka tashi zuwa bakin fada.*

*Les notables et l'imam retourent à la place du chef.*

Sarki *(Ya kira Liman)* : Limam!

Le roi *(Appelle l'imam)* : L'imam!

Kalla: Limam, limam!

Kalla: L'imam, l'imam!

Limam: Ahan!

L'imam : Ah, oui!

Kalla: Tsaya yana kira.

Kalla : Il veut te parler.

Sarki: Kalla tasan ni.

Le roi : Aide-moi à me lever.

Limam: Allah ba ka nasara!

L’imam : Votre Majesté !

Sarki: Limam!

Le roi : L’imam **!**

Limam: Na’am!

L’imam : Oui !

Sarki: Ka san hwadawa, taɓarya ne.

Le roi : Tu connais bien les notables, ils sont comme le pilon.

Limam: Insha Allahu!

L’imam : Bien sûr !

Sarki: Mai baki biyu.

Le roi : Qui a deux têtes**.**

Limam: Wannan gaskiya ne.

L’imam : Ça c’est la vérité.

*Sarki yana magana Kalla yana gyaggyara masa hula da riga..*

*Le roi prend la parole et Kalla lui arrange son habillement*

Sarki: An kana nan kai ne. An baka nan ba kai ba ne. Na baka amana ɗana Ɓaidu ga shi nan. A riƙe amana liman.

Le roi: Si tu es là, c’est toi et à ton absence ils changent. Je te confie mon enfant Baidou. Tiens parole limam.

Limam: Amana na riƙe hal lahira.

L’imam: J’enprends l’engagement jusqu’à ma mort.

Sarki: A riƙi amana limam, a riƙi amana limam.

Le roi : Prends soin de lui l’imam, prends soin de lui l’imam.

Sarki: Kalla!

Le roi : Kalla !

Kalla: Allah baka nasara!

Kalla : Votre Majesté !

Sarki: Kwantan ni!

Le roi : Aide-moi à me coucher !

Kalla: Allah baka nasara!

Kalla : Gloire à vous !

*Kalla ya kama sarki ya kwantar da shi saman shimfidarsa ya rufe shi.*

*Kalla aide le roi à se coucher sur son matelas et le couvre d'un drap.*

Limam: Biya maradi kana jin abin da tsohonka ya hwaɗì?

L'imam : Mon prince tu as entendu ce que ton père vient de dire ?

Ɓaidu: Ina ji, gafarta malam, ni mutawa, mutuwa, mutuwa ce yau ma, yau ma a shirye nike

Baidou : J'ai bien entendu, votre Eminence, moi c'est sa mort, sa mort, même audjourd'hui, aujourd'hui même je suis prèts.

Limam: A'a!

L'imam : Non !

Ɓaidu: Yau ma in ya mutu ni ne.

Baidou : Même aujourdhui s'il meurt c'est moi.

Kalla da limam: A'a! A'uzu Billahi!

Kalla et l'imam : Non ! Que Dieu nous preserve !

Limam: Haba, Ɓaidu kai da ake so a wa jigon gidan nan, kuma za ka faɗì wannan? Ai, ai ba sai ka faɗì ba.

L'imam : Ah, Baidou toi à qui on veut confier ce palais, c'est toi qui parles ainsi ? Mais, mais tu n'as pas à le dire.

Ɓaidu: A shirye nike ni.

Baidou : Je suis prèt.

Limam da Kalla: Jeka tahi! Tashi! Tashi jeka! Tahi gidan Magaram ka yi jira na can.

L'imam et Kalla : Vas-y ! Lève-toi, lève-toi et vas- t-en. Vas chez Magarame tu m'attends là-bas.

Ɓaidu:Tau !

Baidou : D'accord !

*Ɓaidou ya fita daga cikin ɗakin. Limam yana jan tabzi ya tashi ya ƙara tofa wa sarki addu'a.*

*Baidou sort de la chambre. L'imam tirant son chapelet se lève et fait encore des invocations au roi.*

Limam: Um! Bari in ƙara mai adda'a. Jakadiya ɗauke wannan.

L'imam : Hum ! Je vais encore lui faire quelques invocations. Jakadiya prend ça.

*Jakadiya ta ɗauke kwano. Kalla ya leƙa sarki, ya tattaɓa shi, ya duba idonsa don ya ga halin da yake ciki.*

*Jakadiya reprend la tasse. Kalla jette un coup d'oeil sur le roi, le touche, regarde ses yeux pour constater son état.*

Kalla: Gafarta malam!

Kalla : Votre Eminence !

Limam: Na'am!

L'imam : Oui!

Kalla: Ai ina zaton…. gani nike idon ya yi hwari, ko barci ne ya samu?

Kalla : Je pense que… comme si  ses yeux sont devenus blancs, peut être qu'il s'est endormi.

*Limam ya tashi ya duba sarki.*

*L'imam se lève et jette un coup d'œil sur  le roi.*

Limam: Kalla!

L'imam : Kalla!

Kalla: Gafarta malam!

Kalla : Votre Eminence !

Limam: A kawo ruwa.

L'imam : Amène de l'eau.

Kalla: Jakadiya!

Kalla : Jakadiya !

Jakadiya: Na'am!

Jakadiya : Oui !

Kalla: A kawo ruwa.

Kalla : Amène de l'eau.

*Jakadiya ta kawo ruwa limam ya amshi ruwan ya shafe wa sarki ido.*

*Jakadiya amène de l'eau et la remet à l'imam qui ferme les yeux du roi avec.*

Limam: La'ilaha Illalahu Mahamadu Rasulilla Wahadahu Lasharika Lahu!  La'ilaha Illalahu!

L'imam : Il n'y a de divinité qu'Allah et Mohammed est son messager.

Kalla: Ya mutu!

Kalla : Il est mort !

Jakadiya: Ya yi mi?

Jakadiya : Ça veut dire quoi ?

Kalla: Sarki ya mutu.

Kalla : le roi est décedé.

Jakadiya: La'ilaha Illala Mahamadu Rasulilla (SAW)!

Jakadiya : Il n'y a de divinité qu'Allah et Mohamed est son messager (PSL)!

*Sarki ya mutu, Jakadiya ta yi cikin gida tana kuka, mata suka fara kuka da buɗa. Limam da Kalla suka lulluɓe sarki cikin dara. Wasu fadawa suka fita da gawarsa. A fadar sarki aka fara buga tambari shaidar sarki ya mutu.*

*Le roi est décedé, jakadiya rentre dans la maison en pleurant, les femmes aussi commencent à crier. L'imam et Kalla couvrent le roi avec une couverture. Certains Les notables sortent avec la depouille. A la place du chef les tambours resonnent annonçant le decé du roi.*

Limam: La'ilaha Illala! La'ilaha Illala! La'ilaha Illala! La'ilaha Illala! La'ilaha Illala! La'ilaha Illala! La'ilaha Illala! La'ilaha Illala! La'ilaha Illala!

L'imam : Il n'y a de divinité qu'Allah ! Il n'y a de divinité qu'Allah ! Il n'y a de divinité qu'Allah ! Il n'y a de divinité qu'Allah !

**TABLEAU II**

*Fadawa sun taru ƙofar sarki wasu a tsaye wasu a zamne don yin shawarar zaɓen wanda zai gaji sarki.*

*Les notables se rassemblent à la place du chef pour designer l'héritier.*

Waziri: To hwadawa ƴan uwana…

Waziri : Mes frères les notables…

Fadawa: Gaskiya ne, gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité, c'est la vérité **!**

Waziri: Ba zama biyu ba za mu biyu…

Waziri : On ne va pas se réunir deux fois…

Fadawa: E!

Les notables : Oui !

Waziri: Tunda mun taru…

Waziri : Puisque nous nous sommes reunis…

Fadawa: Unhum!

Les notables : Oui !

Waziri: Ya kamata hwa gidan nan hwa a yi mai jigo.

Waziri : Le mieux c'est d'élire un héritier.

Fadawa: Hum! Gaskiya ne. Gaskiya ne.

Les notables : Hum ! C'est la vérité, c'est la vérité.

Limam: Wane irin jigo za a yi? Gida da yana da jigo. Da margyayi da zai mutu ya ce ga Ɓaidu, kuma ka yi wani jigo daban?

L'imam : Quel héritier? On a déja un héritier. Le roi avant de mourir nous a confié son fils Baidou, et tu parles d'un autre héritier ?

Fadawa: Ikon Allah! Ikon Allah!

Les notables : Dieu est grand ! Dieu est grand !

Ciroma: Assha! Limam wace irin magana ce kake yi wannan? Yau Ɓaidu shi kaɗai ne ɗan sarki gidan nan?

Tchiroma : Désolé ! L'imam de quoi parles-tu ? Baidou n'est pas le seul prince dans cette cour?

Fadawa: Unhum! Unhum!

Les notables : Oui ! Oui !

Ciroma: Shaho, shi ne babbansu, ɗan sarki ne.

Tchiroma : Chafo, est lui l'ainé, il est un prince.

Fadawa: Um, ƙwarai kuwa.

Les notables : Oui, c'est la pure vérité.

Ciroma: Ga maina Mushe, shi ma ɗan sarki ne.

Tchiroma : Il y a maina Mouché, il est un prince.

Fadawa: Hum! Ƙwarai da gaske!

Les notables : Houm ! C'est la vérité !

Ciroma: Juju ma ɗan sarki ne, dan dai ƴan uwa sun shiga gabanshi.

Tchiroma : Joujou aussi est un prince. C'est parcequ'il est victime de sorcelerie.

Fadawa: Yauwa!

Les notables : Bien dit !

Ciroma: Maina Salihi!

Tchiroma : Le prince Salihi !

Fadawa: Ɗan Baƙoshi, Ɗan Baƙoshi.

Les notables : Le fils de « « Bakoshi », le fils de « Bakoshi ».

Ciroma: A zamanin ubanshi ba mu da yunwa.

Tchiroma : Au temps de son père nous n'avons pas faim.

Fadawa: Gaskiya ne. Insha Allahu! Insha Allahu! Ba mu da yunwa, ba mu da ƙishirwa.

Les notables : C'est la vérité. Si Dieu le veut bien ! Si Dieu le veut bien ! On n'a ni faim, ni soif.

Ciroma: Ka ce muna waye, waye gida yana da jigo? Yaushe aka yi mashi jigo?

Tchiroma : Et tu nous dis qu'on a un héritier ? Dépuis quand on l'a élu ?

Limam: Ashe gaskiya margyayi da ya hwaɗi. Ya ce : « ku hwadawa taɓarya ce mai baki biyu. »

L'imam : Le défunt roi a raison, quand il dit que vous les notables vous êtes comme le pilon qui a deux têtes.

Galadima: Hum, ba taɓarya ba ce me baki biyu ba limam, yada za ku gane, kowa kun yi abun da ya kamata na gargajiya. Sabada, da nan gidan, da dogarai da bayun sarki suke naɗa sarki.

Galadima : Houm, ce n'est pas question de pilon à deux têtes l'imam, ce que vous devrez comprendre ; chacun de vous a fait ce qu'il faut faire de la tradition. Puisque avant, dans cette cours c'est les notables et les serviteurs du roi qui désignent l'héritier.

Fadawa: Haka ne ƙwarai ko, insha Allahu!

Les notables : C'est bien ça, si Dieu le veut bien !

Waziri: An kawo zamani ya zo na turawa suke kawowa mutun ko ba ɗan gidan sarautal ba ne, wanda bai gaji sarautal ba iyaye da kakannu aka a sa shi gidan in dai yana masu ɗan wani abu sai su kawo su sa shi.

Waziri : Nous sommes au temps où les blancs placent les gens qu'ils veulent même s'ils ne sont pas des princes, pourvu qu'ils obeissent à leurs ordres.

Fadawa: Abin da aka yi ne kowa ya sani. Kowa ya sani kwarai kuwa.

Les notables : C'est ce qui s'était passé. Nous le savons tous.

Waziri: To aka zo aka bar wannan zamani ya komo yanzu, zamani ne na siyasa.

Waziri : On a tout laissé, nous sommes aujourdhui au temps de la politique.

Fadawa: Shakka babu.

Les notables : Sans aucun doute.

Waziri: Babu wani abu in mutun bakka siyasal ko kai ɗan saraul ne in mutun kakan, kakanka sarki ne ba a maka.

Waziri : Il n'y a rien si tu ne fais pas de la politique même si tes grands parents ont régné on ne te nomme pas.

Fadawa: Haka ne, gaskiya ne.

Les notables : C'est ça ! C'est la vérité.

Waziri: Abin da ya sa, sabada kowane allazi da na shi amanu.

Waziri : Ce qui est à la base est qu'à temps nouveau attittude nouvelle.

Fadawa: Ƙwarai ko haka ne!

Les notables : Bien sûr, c'est çà !

Waziri: In mutun ɗan siyasa ne ake ɗauka a sa shi a naɗa.

Waziri : Si tu es politicien on te prend et on te nomme.

Fadawa: Insha Allahu!

Les notables : Si Dieu le veut bien !

Waziri: To kai limam ka zo da wani gemanka yawa wutsiya shaho ka ce za a kawo mutun da rana kai tsaka ka ce za a sa shi sarauta.

Waziri : Toi l'imam tu viens avec ta barbe on dirait la queue d'un épervier et tu nous imposes quelqu'un qui n'est pas prince.

Fadawa: Au yo wannan zance ne? Zance ne?

Les notables : Ça c'est un bon propos ? C'est un propos ça ?

Galadima: Waziri, Waziri ko baya ji na?

Galadima : Waziri, Waziri tu ne m'entends pas ?

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Galadima: Ka ga yanzu da kai waziri da limam da Ciroma yau kune manya a gidan nan.

Galadima : Tu vois waziri, l'imam et Tchiroma vous êtes les sages de cette cour.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C’est la vérité !

Galadima: Ko?

Galadima : Ou bien ?

Fadawa: Gaskiya ne, gaskiya ne!

Les notables : C’est la vérité ! C’est la vérité !

Galadima: Bai kamata ba a tsakaninku kuna tantonawa yara suna gani.

Galadima : Ce n’est pas normal de tirailler entre vous et les enfants vous observent.

Waziri: A’a, limam salla ce ta shi. Mune manya, mune manya.

Waziri : Non, le rôle de l’imam est de donner la prière. Nous sommes les grands, nous sommes les grands.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C’est la vérité !

Galadima: Shi ma yana cikin manya.

Galdima : Lui-même il est parmi les grands.

Fadawa: Insha Allahu!

Les notables : Si Dieu le veut bien.

Galadima: Yo! Yo! Amma zancen da kake yi ai zancen kumandan ne ko?

Galadima : Mais ! Mais ! Mais vous parlez du commandan, non ?

Waziri: Um!

Waziri : Oui !

Galadima: To ai Shadaɗi jiya ya zo ya ce mini yanzu yake zauwa.

Galadima : Mais hier « Chadadi » me disait qu’il viendra aujoud’hui.

Fadawa: Suparepan ko?

Les notables : Le Sous-préfet ?

Galadima: I!

Galadima : Oui !

Waziri: To ai ba laifi ba ne. Allah ka shi lahiya.

Waziri : Ce n’est pas grave. Que Dieu l’amène en bonne santé.

Fadawa: Ya zo mana, ya zo mana.

Les notables : Qu’il vienne, qu’il vienne.

Shara: Ka gani Galadima, ai suparepan ya zo, ga shi nan a bakin ƙohwa.

Chara : Tu vois Galadima, le sous-préfet est là, il est à la porte.

Waziri: A zo a ɗauko kujera.

Waziri : Allez-y chercher une chaise.

Fadawa: To!

Les notables : D'accord !

Waziri: E!

Waziri : Oui !

*Kumandan ya shigo tare da kumandan ƙarami da wani soji a gabansu. Kowa da kowa ya tashi tsaye ana gaisawa.*

*Le commandant arrive avec son adjoint sous l'escorte d'un garde. Tout le monde se lève pour les salutations.*

Fadawa: Ranka ya daɗe! Ranka ya daɗe! Sannu da zuwa. Sannu-sannu hwa.

Les notables : Longue vie à toi ! Longue vie à toi ! Bien venue.

Kumandan: Sai ku zamna.

Commandant : Assayez-vous.

Maroƙi: Ku zamna jama'a, a zamna.

Le griot : Assayez-vous, assayez-vous.

Limam: Alhamdu Lillahi Rabil Alamin. Fatiya!

L'imam : Récite la fatiya.

Fadawa: Amin, amin!

Les notables : Amen ! Amen!

Limam: Fatiya!

L'imam : Invocations !

Fadawa *(Gaba ɗaya suka shafa fatiya) :* Fatiya, amin, amin liman!

Les notables *(Passent sur leur corps)* : Invocations, amen, amen l'imam !

Limam: Ina gida? Kuna lafiya? Lahiya lau hwa. Madalla ina mataiku? Ina su Hajiya? Madalla!

L'imam : Comment va la famille ? Vous allez bien ? Merci et vos femmes ? Et les Hadjia ? Merci.

Kumandan ƙarami: Muna lahiya? Lahiya lau hwa.

Adjoint au sous-préfet : Répond aux salutations.

Limam: Lahiya lau hwa. Ina ƴan dugur dugur? Na san da ana kai ana kawowa.

L'imam : Dieu merci. Comment vont les petits ? Je souhaite qu'ils se portent bien.

*Kumandan da kumandan ƙaramin suka zamna bisa kujeru. Bayan haka kumandan ya hiddo kuɗi daga aljihunsa yaba Liman.*

*Le sous-préfet et son adjoint prennent place. Après le sous-préfet sort de l'argent de sa poche et le remet à l'imam.*

Limam *(Yaƙi karɓar kuɗin):* A'a haba, Kumandan! Madalla.

L'imam *(Limam refuse de prendre l'argent)* : Non, non, mon commandant ! Merci !

Kumandan ƙarami : Limam amshi mana. Amshi ! Karɓi limam.

Adjoint au sous-préfet: L'imam prend ! Prend ! L'imam prend !

Kumandan: Ina abun da ya samu?

Commandant : Mes condoléances.

Fadawa: An gode, e, an gode. Ai kumandan ƙarami duk komi da shi aka yi.

Les notables : Merci, oui, merci. Tout s'est passé en présence de votre adjoint.

Fadawa: Haka ne.

Les notables : C'est comme ça.

Waziri: Komi da komi duka abun da yakamata komi kaman kana nan da shi aka yi.

Waziri : Tout s'est passé en présence de votre adjoint. Il a tout fait, comme si tu étais présent.

Fadawa: Ƙwarai ko,  gaskiya ne. Insha Allahu!

Les notables : Bien sûr ! C'est la vérité. Si Dieu le veut bien !

Kumandan: Ina can an kire ni wurin shawara.

Commandant : J'étais làbas on m'a convoqué à une réunion.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Kumandan: Sai aka ce mina ai sarkin nan ya zan babu.

Commandant : C'est làbas que j'ai appris le decés du roi.

Fadawa: Insha Allahu! Gaskiya ne!

Les notables : Si Dieu le veut ! C'est la vérité !

Kumandan: Kwana na yi ina tahiya.  Kuma da na zo sai "adjoint" ma ya bani wasu takardu.

Commandant : J'ai passé la nuit à rouler. En venant mon adjoint m'a remit certains papiers.

Waziri: Tau!

Waziri : D'accord !

Kumandan: Ya ce mini ga waɗanda suka tambayi sarauta nan a ciki sunayensu.

Commandant : Il m'a dit que c'est la liste des candidats à la chéfferie.

Waziri: Yau tun kamin ya mutu kenan ya bada?

Waziri : Donc il a envoyé la liste avant de mourir ?

Kumandan ƙarami: Ku tsaya, waziri.

Adjoint: Attendez, Waziri!

Waziri: Tau!

Waziri : Oui !

Kumandan ƙarami: Abin nihi a ciki, lokacin da aka yi rasuwa a cikin mainawa…

Adjoint : Il faut comprendre que au moment du decés, parmis les héritiers…

Waziri: Ai!

Waziri : Oh !

Kumandan ƙarami: Akwai wa'anda suka kai takardu da sunan suna son sarauta.

Adjoint : Il y a ceux qui ont envoyé leur candidature.

Waziri: I, tau!

Waziri : Oui, d'accord !

Kumandan ƙarami: Shi ya sa ba zan iya yin wani abu ba sai da na tsaya ya zo tukun na gwada mashi.

Adjoint : Comme je ne peux pas decidé seul, c'est pour quoi j'ai attendu l'arrivée du sous-préfet pour lui montrer.

Fadawa: Gaskiya ne.

Les notables : C'est ce qui est juste.

Kumandan ƙarami: Shi ya ce mu taho nan.

Adjoint : C'est lui-même qui a demandé à ce qu'on vienne ici.

Waziri: Ka yi ladabi, ka yi ladabi. Yanzu ka gaya mamu sunan mutanen da suka tambaya.

Waziri : Tu as été poli, tu as été poli. Maintenant dis nous le nom des princes qui ont demandé.

Kumandan ƙarami: I, mana!

Adjoint : Oui, bien sur !

Waziri: Yauwa ai gara mu ji sabada ko an yi wata mantuwa.

Waziri : C'est mieux qu'on nous le dise, il est possible que vous ayez oublié certains noms.

Fadawa: Ko shakka babu, ai, ai. Gaskiya ne!

Les notables : C'est certain, oui, oui, vous avez raison.

Kumandan *(Riƙe da takarda mai sunayen mainawa a hannunsa)*: E, to! A cikinsu akwai maina Mushe.

Commandant *(Tenant la liste des prétendus hériters)* : Eh, oui ! Parmi eux, il y a maina Mouché.

Fadawa: I, gaskiya ne, ɗan sarki ne.

Les notables : Oui, c'est vrai, c'est un prince.

Kumandan: Akwai maina Shaho.

Commandant : Il y a maina Chafo.

Fadawa: Shi ma ɗan sarki ne.

Les notables : Lui aussi c'est un prince.

Kumandan: Akwai maina Ɓaidu.

Commandant : Il y a maina Baidu.

Fadawa: E, maina Ɓaidu kenan?

Les notables : Oui, maina Baidu.

Waziri: Suke nan?

Waziri : C'est tout ?

Kumandan: E, suke nan.

Commandant : Oui, c'est tout.

Waziri: An yi mantuwa, an yi mantuwa, ƙwarai kwa.

Waziri : Il y a eu un oubli, il y a eu un oubli, bien sùr.

Kumandan ƙarami: Kama ta mi hwa?

Adjoint : Comme quoi ?

Waziri: Mantuwa ita ce muna da wani maina, shi ma wanda ya kulla da du irin abin da kuke so na nan a garinmu. Shi ne dai ku tammaninku suke siyasa ko?

Waziri : L'oubli est que, nous avons un prince qui s'occupe de tout ce que vous voulez dans notre village. Selon vous, c'est celui qui fait la politique non ?

Kumandan ƙarami *(Ya amshi takardar ya duba)* : E, ƙwarai ko.

Adjoint *(Prend le papier et regarde) :* Oui, bien sur.

Waziri: To, yana tsaka daga cikin masu yin ta.

Waziri : Donc il est parmi ceux qui la font.

Fadawa: E, ƙwarai!

Waziri : Bien sur !

Waziri: Mutun ne wanda ubansa ya jiya muna daɗi ƙwarai, mu yi hatsi, mu yi dawa, wake, shinkahwa babu abun da bama yi a lokacin ubansa.

Fadawa: Ƙwarai ko!

Les notables : Bien sur !

Waziri: Kuma banda haka nan wani cuta wani lalata du ba mu yin ta a wannan ƙasa.

Waziri : C'est quelqu'un dont le père nous a bien entretenu, nous cultivons du mil, sorgho, haricot, riz, il n'y a pas ce que nous ne cultivons pas au temps de son père. Et à part ça nous ne faisons aucune délinquance.

Fadawa: Ƙwarai ko! Allah ya kore, Allah ya kore. Ƙwarai kuwa.

Les notables : Bien sur ! Dieu nous a épargné, Dieu nous a épargné. Bien sur !

Waziri: To shi ne Salihi.

Waziri : Donc c'est Salifi.

Fadawa: Ɗan Baƙoshi.

Les notables : Le fils de « Bakoshi.»

Waziri: Um!

Waziri : Oui !

Kumandan ƙaramin: Waziri ba mantuwa ba ce aka yi

Adjoint : Waziri ce n'est pas un oubli.

Waziri: Um!

Waziri : Oui !

Kumanadan ƙaramin: Wato wa'annan mainawa da ka ji sunansu aikawa suka yi.

Adjoint : Ces princes là ils ont envoyé leur nom.

Waziri: Um!

Waziri : Oui !

Kumandan ƙarami: Shi wannan wanda ka faɗi…

Adjoint : Celui là dont tu viens de dire le nom…

Waziri: Salihi!

Waziri : Salifi !

Kumandan ƙarami: Wake sunanshi?

Adjoint : Comment il s'appelle ?

Fadawa: Salihi!

Les notables : Salifi !

Kumandan ƙarami: Shi Salihi abun da ya sa ba ka ba ji sunanshi ba, sabada shi bai gwada ba iya so.

Adjoint : Tu n'as pas entendu son nom parcequ'il n'a pas montré qu'il est interessé.

Fadawa: Ba ya gwadi ba. Kunya gare shi, iyayenshi da kakanninshi kunya suka gada.

Les notables : Il ne peut pas le montré. Il a honte, il l'a hérité de ses parents et grands parents.

Waziri: To amma yanzu abin da muke so kumandan ƙarami…

Waziri : Ce que nous voulons maintenant adjoint…

Kumanadan ƙarami: Tau!

Adjoint : Ok !

Waziri: Ka yi ƙoƙari ka rubuta mumu shi.

Waziri : Il faut tout faire pour nous l'inscrire.

Kumandan ƙarami: To!

Adjoint : Ok !

Waziri: In yaya za a yi, ya dai ya samu sarautal nan. Ka dai rubuta shi, kai ɗai.

Waziri : Quelqu'en soit ce que vous faites pourvu qu'il soit élu. Il faut l'inscrire.

Kumandan ƙarami: Za a rubuta shi.

Adjoint : On va l'inscrire.

Fadawa: E, ka rubuta shi.

Les notables : Oui, il faut l'inscrire.

Kumandan ƙarami: To, yaya ne sunan tsohon nashi?

Adjoint : Donc comment s'appelle son père ?

Fadawa: Tsohonshi Baƙoshi.

Les notables : Son père s'appelle « Bakoshi. »

Kumandan ƙarami: A'A! Oui! Oui! Na ga sunanshi, na ga sunanshi.

Adjoint : Ah ! Ah ! Oui ! J'ai vu son nom, je l'ai vu.

Kumandan: Sunan ne kenan?

Adjoint : C’est le nom comme ça ?

Juju *(Ya zo wajen taron)*: Kumandan ni ma ina so.

Joujou (*Arriveà la réunion) :* Mon commandant moi aussi je suis candidat.

Fadawa: Ikon Allah!

Les notables : Par Dieu !

Juju: Kumandan ba ka san ni ba?

Joujou : Commandant tu ne me connais pas ?

Kumandan: Wannan hwa?

Commandant : Et celui là ?

Fadawa: An ji kana so. Kai ne kumandan zai ma.

Les notables : C’est entendu. C’est toi que le commandant va nommer.

Juju: To ni akawa ko?

Joujou : C’est moi qu’on a choisi ?

Waziri: E, mu je.

Waziri : Oui, allons-y !

Juju: To in tahi? To in tahi.

Joujou : Donc je peux partir ? Je peux partir ?

Waziri: Mu jeka, mu je.

Waziri : Allons-y !

Kumandan ƙarami: Shi wannan wane ne?

Adjoint : C’est qui celui là ?

Waziri: Ƴan uwa suka shiga gabansa.  Shi ne maina Juju. Shi ma ɗan sarki ne.

Waziri : Il a été ensorcellé par ses frères. Il s’appelle Joujou, c’est un prince aussi.

Kumandan ƙarami: Kai Allah ya kiyaye mu.

Adjoint : Que Dieu nous en garde.

Fadawa: Amin, amin!

Les notables : Amen ! Amen !

Kumandan ƙarami: Allah ya kiyaye mu.

Adjoint : Que Dieu nous en garde.

Waziri: To abin da muke so yanzu kumandan ƙarami shi ne ka san zamanin wannan, sai a zo dai da wuri wuri a yi sha'anin nan.

Waziri : Ce que nous voulons adjoint, c'est de venir vite faire les élections, vous savez bien que nous sommmes en période de politique.

Kumandan: Waziri ka san in muka tahi…

Commandant: Waziri tu sais, en allant…

Waziri: Tau!

Waziri : Oui !

Kumandan: Zan zo tare da purepe, ka san sai da babbana ni ma zan zo.

Commandant : Tu sais, il faut la présence de notre chef. Donc je reviens avec le préfet.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : Tu as raison !

Kumandan: Sabada a naɗa saban sarkin naku.

Commandant : Pour qu'on puisse élire votre nouveau roi.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : Tu as raison !

Kumandan: To amma yanzu…

Commandant : Mais maintenant…

Waziri: E!

Waziri : Oui !

Kumandan: Kan mu zo…

Commandant : Avant notre arrivée…

Waziri: Tau!

Waziri : Oui !

Kumandan: Tunda kai ne babba kan muzo kai zaka kulawa da dukan abubuwan.

Commandant : Puisque tu es l'ainé tu vas tout organiser avant notre arrivée.

Waziri: To, toi nsha Allahu.

Waziri : Ok ! Si Dieu le veut bien.

Kumandan ƙarami: Duk abun da ya hwaru kai ne.

Adjoint : Tu seras responsable de tout ce qui adviendra.

Waziri: Gaskiya ne!

Waziri : C'est la vérité !

Kumandan: E, kai ne.

Commandant : Oui, tu seras responsable.

Kumandan ƙarami: Milki hwa a hannunka yanzu, du abun da ya hwaru kai ne.

Adjoint : Maintenant le pouvoir est entre tes mains, tu seras responsable de tout ce qui adviendra.

Waziri: Gaskiya ne, na gode.

Waziri : Tu as raison, merci.

Kumandan karami: E! E!

Adjoint : Oui ! Oui !

Waziri: To kuma bayan wannan muna so a zo da wuri a yi muna sarauta, kun san sabada karo, sarki hwa in babu shi karo ba ya amsuwa.

Waziri : C'est pour quoi nous voulons qu'on vienne vite élire le nouveau roi, vous savez qu'on ne peut pas collecter l'impôt s'il n'y a pas de roi.

Fadawa: Gaskiya ne, gaskiya ne.

Les notables : Vous avez raison.

Kumandan: Amma yanzu kan muzo, kai za ka kullawa da mutane.

Commandant : Mais maintenant avant notre arrivée, tu vas assurer l'intérim.

Kumandan ƙarami: Komi yana a hannunka, komi ya hwaru kai ne.

Adjoint : Tout est entre tes mains, tu seras responsable de tout ce qui adviendra.

Fada: Gaskiya ne!

Les notables: Vous avez raison !

Galadima**:** Waziri, a gargaɗi limam.

Galdima: Waziri, il faut mettre l'imam en garde.

Waziri: A'a, wannan kuma, gargaɗin mi za a mashi, wannan ƙyale kai.

Waziri : Non ! Ça aussi, pour quoi le mettre en garde, laisse le.

Galadima: A gargaɗe shi.

Galdima : Il faut le mettre en garde.

Waziri: Ba dai garin a hannuna ba yake?

Waziri : C'est moi qui assure l'intérim non ?

Galadima: A'a to!

Galadima : Ah, oui !

Waziri: Gargaɗin mi za a yi mishi?

Waziri : Pour quoi lui faire une mise en garde ?

Kumandan ƙaramin: Waziri za mu wuce ni da kumandan sabada akwai wani gari da aka yi hwaɗa na gona.

Adjoint : Waziri, nous allons prendre la route puisqu'il y a un conflit champêtre dans un autre village.

Waziri: To insha Allahu!

Waziri : Si Dieu le veut bien !

Kumandan: To waziri, sai an jima. Limam.

Sous prefet : Donc Waziri à tout à l'heure. L'imam.

Waziri: To!

Waziri : D'accord !

Fadawa: Tau, tau, insha Allahu to ranka ya daɗe, sai an jima.

Les notables : D'accord, d'accord, si Dieu le veut bien, longue vie à vous, à la prochaine.

Kumandan da kumandan ƙarami: Tau waziri, sai an jima.

Adjoint et commandant : Waziri ça fait à la prochaine.

Waziri: A shahi kan yara.

Waziri : Bien de choses aux enfants.

Kumandan ƙarami: Limam sai an jima.

Adjoint : L'imam à tout à l'heure.

Limam: To!

L'imam : D'accord !

*Kumandan da kumandan ƙaramin suka tashi za su tafiya duk mutane suka tashi tsaye, suka ba kowa hannu sa'annan suka fita daga fada,*

*Le* commandant *et son adjoint se retirent, tout le monde se lève et leur font des au revoir*

Limam: Wai yanzu ha ni limam a fada waini ba komi ba ne. Ni za a maidawa kama yaro.

L'imam : Maintenant c'est moi l'imam qu'on va rediure au néant. On me prend pour un enfant.

Waziri: Fada ai ba masalaci ba ce, wurin salla nan ne za ka gwada kai limami ne. Ka yi karatu.

Waziri : La cour royale n’est pas comme la mosqué, c’est à la prière que tu vas nous montrer que tu es iman, tu sais faire plus que nous. Tu as lu le coran.

Fadawa: Shakka babu!

Les notables : Sans aucun doute !

Waziri: Ka sabka, ka zo ka yi harda.

Waziri : Tu as lu les soixente verserts du coranet tu les a revisé.

Fadawa: Ƙwarai kuwa!

Les notables : C’est ça !

Waziri: Nan gidanmu ne.

Waziri : Ici c’est chez nous.

Fadawa: Kai ba kowa ba ne.

Les notables : Tu n’es rien.

Waziri: Nan ƙofar fada ce, wurin fada.

Waziri : Ici c’est la cour royale, c’est pour les notables.

Fadawa: Wurinmu ne. Mune fada, kai ba kowa ba ne, mune fada.

Les notables : C’est notre place. Nous sommes les notables, tu n’es rien.

Waziri: Kai, ina anhwanin tankiya? Kai!

Waziri : Ce n’est pas la peine, pour quoi tant de tiraillement ?

*Fadawa suka fara gardama, taron ya waste.*

*Les notables commencent à se disputer et la réunion se termine mal.*

**TABLEAU III**

*Alhaji ya shigo gidan mushe ya tarda shi yana aiki da takardu bisan teburinsa na aiki yana ta rubutu.*

*Elhadji trouve Mouché chez lui entrain de travailler sur son bureau rempli de papiers.*

Alhaji: Salamu alaikum! Salamu alaikum!

Elhadji : Que la paix soit avec vous ! Que la paix soit avec vous !

Mushe: Amin, alaikum wassalam!

Mouché : Amen, à toi de même !

Alhadji: Mushe!

Elhadji : Mouché !

Mushe: A, Alhaji!

Mouché : Ah, Elhadji !

Alhaji: Muna lahiya?

Elhadji : Comment tu- vas ?

Mushe: Lahiya lau!

Mouché : Je vais bien !

Alhaji: Lahiya lau!

Elhadji : Ça va  bien.

Mushe: Lahiya lau, zamna Alhaji!

Mouché : Bien, Elhadji prends place !

Alhaji: A! To!

Elhadji : Ah ! Oui !

Mushe: Ina nan ina rubutu naka jin sallama, ka san yanzu cikin aiki muke. Yaya, « ça va »dai?

Mouché : Je suis entrain de travailler, c'est la période des travaux. C'est comment ? Ça va bien ?

Alhaji: Mu ƙara gaisawa. Lahiya sannu-sannu.

Elhadji : On se salue encore. Très bien.

Mushe: Ina zuwa da komowa?

Mouché : Et les va-et-vients ?

Alhaji: A'a! Alhamdu lillahi to madalla!

Elhadji : Non ! Dieu merci !

Mushe: Yaya wajen aikin sana'a?

Mouché : Ça va, Dieu merci. Et le commerce ?

Alhaji: Alhamdu lillahi!  Ina can ƙoha kanti sai na ga wannan yaron nawa Hashimu til, til da gudu sai ya ce ai abun ta zo.

Elhadji : J'étais devant ma boutique quand j'ai vu Hachimou venir en courant et me dire que la chose là est arrivée.

Mushe: A, wannan, ail Kanada?

Mouché : Oui, celle qu'on a amenée du Canada ?

Alhaji: I, ail kanada, dawa.

Elhadji : Oui ! La canadienne, le sorgho.

Mushe: A! Dawa? Ta zo wallahi, ta zo, ai yanzu cikin aikinta nike sosai.

Mouché : Ah ! Le sorgho ? Oui, c'est arrivé, je suis entrain de travailler sur ça maintenant.

Alhaji: Yauwa!

Elhadji : Bien !

Mushe: Dan jiya da yau abin da na samu, motoci sun zo, to saidai sauran ba su iso ba.

Mouché : Beaucoup de voitures sont arrivées entre hier et aujourd'hui, mais il reste encore d'autres qui sont en cours de route.

Alhaji: E, kama dubarun naka hwa. Nan kaka hutowa, kana shan iska?

Elhadji : Oui, tu as des astuces. C'est ici que tu viennes te réposer et prendre de l'air

Mushe: Sabada can ma buro in na yi, kuma nan ma gida sai in zo nan ma in yi. "Ça va" dai ko?

Mouché : Parce que même au bureau je travaille et si je ne termine pas je continue à la maison. Ça va, n'est ce pas ?

Alhaji: A! I, mana, aiki yama yawa yanzu, aiki yama yawa.

Elhadji : Ah ! Oui bien sur tu as beaucoup de travail maintenant, tu as trop de travail.

Mushe: To lahiya daiko?

Mouché : Tout va bien n'est ce pas ?

Alhaji: I, yo lahiya amma ba ba komai ba.

Elhadji : Oui, mais pas sans problème.

Mushe: To!

Mouché : Ok !

Alhaji: Saboda kaman kullun "quoi" wannan abun.

Elhadji : Mais comme tous les toujours quoi, la chose là.

Mushe: A! Na gane, na gane. To kaman ƙaƙa ne yau?

Mouché : Ah ! J'ai compris, j'ai compris. C'est comment pour aujourd'hui ?

Alhaji: Saidai wannan gamin hwa da dama nike so.

Elhadji : Seulement cette fois ci j'en veux beaucoup.

Mushe: Da dama Alhaji? Kaman guda nawa?

Mouché : Tu en veux beaucoup Elhadji ? A peu près combien ?

Alhaji: E, kaman wajen ton goma nike so.

Elhadji : Je veux à peu près dix tonnes.

Mushe: Ton nawa?

Mouché : Combien de tonnes ?

Alhaji: Ton goma.

Elhadji : Dix tonnes ?

Mushe: Goma?

Mouché : Dix ?

Alhaji: I!

Elhadji : Oui !

Mushe: Alhaji goma ba ta samuwa.

Mouché : Elhadji tu ne peux pas avoir dix.

Alhaji: Ashe?

Elhadji: A bon?

Mushe: E, don abin da ya sa motocin ba su zo ba duka, akwai wasu da suka tsaya wajen Madawa.

Mouché : Oui, parce que tous les véhicules ne sont pas arrivés, il y a d'autres qui sont restés à Madaoua.

Alhaji: I, yo na sani dai, amma a yi ƙoƙari saboda amfani nike da ita ƙwarai.

Elhadji : Oui, je le sais, mais il faut faire un effort parce que j'ai besoin de ça.

Mushe: I, to, kaman dai yadda muka saba, ba za ka samu ton goma ba, amma dai ina ɗan damarde kaman yadda na saba ma in ba ka bakwai « pour le moment quoi. »

Mouché : Eh, oui ! Comme nous avons l'habitude de le faire, tu ne peux pas avoir dix tonnes, mais pour le moment je vais me débrouiller comme j'ai l'habitude de le faire pour te donner sept pour le moment quoi.

Alhaji: I, amma kuma daga baya sai a batse ko?

Elhadji : Oui, mais après tu vas me completer ?

Mushe: A, to wannan kuma.

Mouché : Oui, mais ça aussi.

Alhaji: To, ai du ɗaya ne, zan baka kuɗin goma duka gaba ɗaya.

Elhadji : C'est la même chose, je vais te donner l'argent des dix d'embler.

Mushe: Duka gaba ɗaya?

Mouché : La totalité ?

Alhaji *(Alhaji ya mika wa mushe damen kuɗi):* I, mana in ya so daga baya sai ka gwaje.

Elhadji *(Elhadji remet à mouché un lot de billets de banque) :* Oui, après tu vas me compléter.

Mushe: Wai, wai, ka san yanzu muna cikin harakokin kuɗi ai yanzu.

Mouché : Oui, oui, tu sais maintenant nous sommes à la recherche de l'argent.

Alhaji: Wallahi!

Elhadji : Je le jure !

Mushe: Wai, wai!

Mouché : Oui, oui !

Alhaji: Ka sani yanzun ma daga wajen banki nake, na ce to tsaya ka gani, kantin ma da na je ban abun nan ba, ban zamna ba ai.

Elhadji : Tu sais, je reviens juste de la banque, j'ai dis laisse voir, quand je suis allé à la boutique je ne me suis, je ne me suis pas resté.

Mushe: To, to da kyau!

Mouché : Ok ! C'est bien !

Alhaji: Um! Um! Gashi daga baya sai ka lissaha.

Elhadji : Hum ! Hum ! Voilà l'argent, après tu vas compter.

Mushe: A'a, ai ba wani lissahi. Ba dai ka…

Mouché : Non, je n'ai pas besoin de compter. Tu as dejà…

Alhaji: Ka yarda da ni kenan ko?

Elhadji : Tu as confience en moi ?

Mushe: Haba Alhaji!

Mouché : Ah non Elhadji !

Alhaji: Yau da gobe sai Allah!

Elhadji : On est toujours ensemble !

Mushe: To ka san yanzu abinda ya sa muna cikin harakoki.

Mouché : Tu sais maintenant nous sommes dans des affaires.

Alhaji: Ƙwarai ko. Yau yaya zancen abun naka?

Elhadji : Bien sur. C'est comment ton affaire ?

Mushe: Zancen sarauta?

Mouché : Affaire de la chefferie ?

Alhaji: E!

Elhadji : Oui!

Mushe: “Oncle”ya yi min waya.

Mouché : Mon oncle m’a téléphoné.

Alhaji: Ka gan shi ko?

Elhadji : Tu l’as vu ?

Mushe: Ya ce in kwanta da hankalina sarauta an dubani za ayi ma.

Mouché : Il m’a dit de ne pas m’inquieter, c’est moi qui serai élu.

Alhaji: To shi kenan.

Elhadji : Donc ça ne fait rien.

Mushe : « Tout est en bonne voix »

Mouché : Tout est en bonne voix.

Alhaji: Daga wajena ni ma ka kwanta da hankalinka.

Elhadji : De mon côté aussi il ne faut pas t’inquieter.

Mushe: Haba, Alhaji!

Mouché : A bon, Elhadji !

Alhaji: Ai ran nan, ran wankan sarauta komi da komi bisa wuyana.

Elhadji : Le jour là, le jour de l’intronisation, je prends tout en charge.

Mushe: A, haba?

Mouché : Ah, bon ?

Alhaji: Na ɗauka, na ɗauka.

Elhadji : Je prends tout en charge, je prends.

Mushe: Haba Alhaji! I, to! Ai ko da ba ka zo ba na zo in gan ka.

Mouché : Ah, bon Elhadji ! Même si tu ne viens pas j’irai te voir.

Alhaji: Inhin!

Elhadji : Ah oui !

Mushe: Saboda lokacin da na samu labarin, za a yi mani sarauta, nace to yanzu ya kamata in kimkimtsa in riƙe wasu abubuwa a hannu.

Mouché : Quand j’ai eu l’information que j’allais être élu, j’ai dis que je dois me préparer et avoir quelques choses en main.

Alhaji: E, ƙwarai da gaske!

Elhadji : Oui, bien sur !

Mushe: Nake son, mota nake so.

Mouché : J’ai besoin, j’ai besoin d’un véhicule.

Alhaji: Wace irin mota? Bagobira ko wace iri?

Elhadji : Quelle marque ? Une Honda ou quelle autre marque ?

Mushe: A’a! A’a! Haba, Alhaji! Ina laihin « Land Robert » a gewaya cikin ƙasa.

Mouché : Non ! Non Elhadji ! Au moins une Land Robert pour faire le tour du pays.

Alhaji: Tsakanin ni da kai, ko shabin dare kwan, kwan, kwan buga min ƙyaure.

Elhadji : Entre nous, même si c’est à minuit tu peux taper toc, toc, toc à ma porte.

Mushe: Haba?

Mouché : Ah, bon !

Alhaji: Mota mi? Kai, haba mota mi tsakanin ni da kai?

Elhadji : C’est quoi une voiture ? Entre nous, c’est quoi une voiture ?

Mushe: Wani abu sai su Alhaji.

Mouché : Certaines choses il faut vous les Elhadji.

Alhaji: A, i, mana!

Elhadji : Ah, mais oui !

*Abokan Mushe, sun zo wajen shi inda suka tarda shi tare da Alhaji. Bayan sun gaisa Alhaji ya tafi,* suka samu wuri suka zamna saman kujeru.

*Les amis de Mouché sont venus chez lui, ils l’ont trouvé en compagnie de Elhadji. Après les salutations Alhaji s’est retiré.*

Mushe *(Abokan Mushe sun shigo):* Wai!

Mouché *(Les amis de mouché font leur entrée*) : Oui !

Alhaji: Ana salama.

Elhadji : On tape à la porte.

Mushe: Wai!

Mouché : Oui !

Alhaji: A! A! Kallamu!

Elhadji : Ah ! Ah ! Kallamou !

Kallamu: Alhaji muna lahiya?

Kallamou : Elhadji tu vas bien ?

Alhaji: Sannu sannu!

Elhadji : Soyez la bienvenue !

Abokan Mushe: Alhaji zamna mana!

Les amis de Mouché : Elhadji prends place !

Alhaji: A'a zamnewa ne ai.

Elhadji : Non c'est une perte de temps

Alhaji, Mushe, Kallamu da Ɗan caram: Muna lahiya? Lahiya layau, yaya kwana biyu?

Elhadji, Mouché, Kallamou da Dan tcharame : Ça ca ? Ça va bien, et tout ce temps ?

Mushe: Ku zamna in dahwa mashi kaɗan.

Mouché : Prennez place, je vais l'accompagner.

Alhaji *(Ya ɗan tsaya) :* Ya mushe Ɗan caram? Rannan kasa na aje turamen atamhwa baka je ba.

Elhadji *(S'arrette un peu):* Mouché Dan tcharame c'est comment ? L'autre fois tu m'as fait reserver des pagnes et tu n'es pas venu.

Ɗan caram: Ba komi Alhaji.

Dan Tcharame : Ça ne fait rien Elhadji.

Alhaji: Ahan, to shi kenan!

Elhadji : Ok, c'est bon !

*Kallamu da Ɗan caram suka zamna suna leƙon ƙarƙashin teburin Mushe.*

*Kallamou et Dan tcharame regardent sous la table de Mouché.*

Mushe: Ka ga wannan Ɗan caram, ka san halinshi? Dan ko ni da ka gani, ina tsoron shi.

Mouché : Dan tcharame là que tu vois, tu le connais ? Parceque je me mefie de lui.

Alhaji: To sai an jima.

Elhadji : Ok, à tout à l'heure.

Mushe: Sabka lahiya.

Mouché : Bonne route.

Alhaji: To sai an jima!

Elhadji : Ok, à tout à l'heure !

Mushe: Ka gaida su.

Mouché : Il faut les saluer.

Alhaji: Um!

Elhadji : Hum !

Mushe *(Bayan ya dawo daga rakiyar Alhaji)* : Ɗan caram mu ƙara gaisawa, muna lahiya?

Mouché *(Vient d'accompagner Elhaji)* : Dan tcharame on se salue encore, vous allez bien ?

Kallamu da Ɗan caram: Lahiya lau. Yaya aikin?

Kallamou et Dan tcharame : Ça va bien ! Et le travail ?

Ɗan caram: Na ga takardu a hannu, yaya aiki?

Dan tcharame: Je te vois avec des papiers, et le travail ?

Mushe: Ai ni ban da buro, da buron da gida du ma'aikata ce.

Mouché : Moi je n'ai pas de bureau, il n'y a pas de différence entre ma maison et mon bureau.

Ɗan caram: Um!

Dan tcharame : Oui !

Kallamu: Du ɗaya ne.

Kallamou : C'est la même chose.

Mushe: Da buron da gida du ma'aikata ce. Tunda ha gida aka zakuwa a ce Mushe gashi-gashi, mun zo gashi-gashi, muna son taimako, gida hwa! Wani bi in na samu dama ne ma'aikata sai in komo nan gida to ban tsira ba.

Mouché : On vient même à la maison pour me dire ceci, cela Mouché, on est venu pour ceci cela, nous avons besoin d'aide, à la maison je vous dis ! De fois si j'ai le temps au bureau je reviens à la maison là aussi je ne suis pas épargné.

Ɗan caram : « Non !»

Dan tcharame :   Non !

Mushe: Har gida hwa aka zakuwa.

Mouché : On me trouve jusqu'à la maison.

Ɗan caram: "Non!" ni gani nika yi wannan « c'est normal », wanda baya da, ina tsammanin, ba abin da ba ya yi. "C'est normal"

Dan tcharame : Non ! Moi je trouve que ça c'est normal, je croix que celui qui est dans le besoin peut tout faire. C'est normal.

Mushe: Mine ne "normal?"

Mouché : Qu'est ce qui est « normal »?

Ɗan caram: Abun nasu ne. Kuma « donc vraiment » wanda bai da, ai bai ji, bai gani.

Dan tcharame : C'est des choses qui leur appartiennent. Et puis vraiment celui qui est dans le besoin il est capable de tout.

Mushe: Mine ne normal kuma?

Mouché : Qu'est ce qui est normal encore ?

Kallamu: Ka ganka ka yi sha'anin da ya kawo mu.

Kalamu : Tu vois, il faut faire ce qui nous a amené.

Ɗan caram: "Non" ba wani abun na ya kawo mu, mun zo, mu ga juma.

Dan tcharame : Non, nous sommes seulement venus te rendre visite.

Mushe: Ka zo min da ƙanƙannan maganganu hakanga « ce n'est pas sérieux »? « En tout cas »Ɗan caram ban san ka da haka ba.

Mouché : Tu me viens avec certaines paroles comme ça, ce n'est pas sérieux. En tout cas Dan tcharam je ne te reconnais pas.

Ɗan caram: Non « ça va » mu yi abun da ya kawo mu.

Dan tcharame : Non, ça va, faisons ce qui nous a amené.

Mushe: Ni na ce na yi kwana biyu ban gan ku ba, ni na ce na yi tahiya wajen « distribution ». Ko ba haka?

Mouché : J'ai voyagé pour faire des distributions et je me plaingnais de ne pas vous voir pendant des jours. Ou bien ce n'est pas ça ?

Kallamu: « Ça va » mu ci gaba da maganamu. Wannan "semaine" kin ba ka sami komi ba?

Kallamou : Ça va, continuons notre causerie. Cette semaine tu n'as rien eu ?

Mushe: « Si, si, » a shekaran jiya ma na komo daga ƙauye. « J'ai fait des distributions la un peu partout » yanzu ɗan « rapport » ne nika nanina yi kuma sabada ina jiran wani kwambuwa kuma.

Mouché : Si, si ! Je suis rentré de la campagne avant-hier. J'ai fais des distributions un peu partout. Maintenant je suis entrain de redigé le rapport parce que j'attends d'autres convois.

Ɗan caram: Kai da kake cewa haka nan ba mun ga Alhaji yana shiga yana hita ba?

Dan Tcharame : Toi qui parles ainsi, nous avons vu Elhadji qui fait des va-et-viens chez toi non ?

Mushe: Wane Alhaji? Kai shi wai Ɗan caram ni ban son irin wannan“indirect” da kakai yi min ka fito sarak ka gaya mani. “Tu veux dire que”ina “affaire”da Alhaji“quoi”?

Mouché : Quel Elhadji ? Dan tcharame je n’aime pas des indirects que tu me fais. Dis-moi clairement ce que tu penses. Tu veux dire que je traite des affaires avec Elhadji ou quoi ?

Ɗan caram: Hum! To tun da ka gayi shi kenan mu ci gaba da haraka.

Dan tcharame : Hum ! Comme c’est toi qui le dis avançons dans notre causerie.

Mushe: Ka tsaya in yi maka zancen aiki, ni nace aiki ya kashe ni, kana mini zancen wani Alhaji. « Si tu veux » kuma Alhajin « affaire » ɗin da muke da shi « c’est normal, comment?”

Mouché : Laisse-moi te parler du travail, je te parle de mon travail et toi tu me parles d’un certain Elhadji. Si tu veux les affaires que je traite avec Elhadji c’est normal. Comment ?

Kallamu: “Non” ba wannan zancen ba na, zancen da muke da shi, mun zo mu ga juna ne, mu yi hira.

Kallamou : Non ce n’est pas ça, ce qui nous amène, nous sommes venus nous rencontrer, nous causer.

Mushe: Ni na yi kwana biyu ban gan ku ba dama ina son…

Mouché : J’ai fais des jours sans vous voir et puis je voulais…

*Almajirai suka shigo tare da sarkin dogarai suna sallama bakin gida sun zo neman taimako wajen Mushe.*

*Les mendiants accompagnés du chef des notables sont venus chercher de l’aumone auprès de Mouché.*

Almajirai: Salamu alaikum!

Les mendients : Que la paix de Dieu soit avec vous !

Mushe: Amin alaikum wassalam!

Mouché : A vous de même.

Mushe: To “voilà, voilà!” Ku gani da idonku. “Voilà!”

Mouché : Eh voilà ! Voilà ! Constatez de vous-même. Voilà !

Almajiri: Mushe!

Un mendiant : Mouché !

Mushe: “Ça va” na gan ka. Ka ku hau bisa tapi, ku zamna nan, ku ja baya, ku ja baya, ku matsa, na ganka“Voilà!”

Mouché : Ça va ? Je t’ai vu. Ne marchez pas sur le tapis, assayez vous là, réculez, réculez, je t’ai vu. Voilà !

Almajirai: Mu ja baya.

Les mendiants : Réculons.

Mushe: « Voilà » yanzu na ƙare ce muku…

Mouché : Voilà je viens juste de vous dire…

Almajiri: Barka Mushe.

Les mendiants : Félicitation Mouché.

Sarkin dogarai: Ya ji, ya gan ku ai.

Lechef desnotables : Il a entendu, il vous a vu non.

Almajirai: Mushe ranka ya daɗe!

Les mendiants : Mouchés longue vie à toi !

Mushe: Kai ma ranka ya daɗe.

Mouché : A toi de même.

Sarkin dogarai: Ka gane su nan…

Le chef des notables : Tu les vois…

Mushe: E!

Mouché : Oui !

Sarkin dogarai: Sun tahi gidan Galadima ya ce a kawo su wurinka.

Le chef des notables : Ils sont allés chez Galadima et c’est lui qui m’a dit de les améner chez toi.

Mushe: To!

Mouché : D’accord !

Sarkin dogarai: Don shi dawa ta wajen shi wadda ka bada a ba su, babu ta ƙare.

Le chef des notables : Le sorgho que tu as envoyé pour leur distribuer est fini.

Mushe: To!

Mouché : D’accord !

Sarkin dogarai: Ta ƙare. Wadda ya sawo, shi, ta shi wadda ya auna da kuɗinshi ma yake ci babu. An yi tuwon, an yi tuwon, an yi tuwon an ba su haka nan kowa sai ya ce bai ƙoshi ba. Daga cikin kashi uku wannan kashi biyu ne ka gani.

Le chef des notables : C'est fini. Même celui qu'il a acheté avec son propre argent est fini. On a tellement preparé du repas pour eux mais à chaque fois ils disent qu'ils ne sont pas rassasiés. C'est les deux tiers des mendiants que tu vois ici.

Mushe: Um! Tau, da kyau.

Mouché : Hum ! Oui, c 'est bien.

Almajiri: Ya ce mu zo mu amshi dawa, ka gani da buhuna na zo.

Un mendiant : Il nous a dit de venir prendre du sorgho, tu vois je suis venu avec mon sac.

Mushe: E, dawa ta zo. Dawa ta zo.

Mouché : Oui, il y a du sorgho. Oui, on a amené du sorgho.

Almajiri: Mushe!

Les mendiants : Mouchés !

Mushe: Kai mine ne?

Mouché : C'est quoi ?

Almajiri: Sadaka.

Un mendiant : L'aumône !

Mushe: Kai ba sadaka ba.

Mouché **:** Pas d'aumone.

Almajiri: Mushe!

Les mendiants : Mouchés !

Mushe: Mine ne?

Mouché : C'est quoi ?

Almajiri: Ni ɗan wasan kura ne ta kada ni.

Un mendiant : Je suis un dompteur d'hyène et elle m'a terrassé.

Mushe: Ta ko raga maka. Da ta kashe ka. Ba ta kada ka ba, ta kashe ka. Ina ruwana ni, kai sarkin dagarai…

Mouché : Elle a mal fait. Elle aurait du te tuer. Ce n'est pas qu'elle t'a terrassé, qu'elle te tue. Ça ne me regarde pas. Et toi chef des notables…

Sarkin dogarai: Ranka ya daɗe!

Le chef des notables : Que Dieu t'accorde longue vie !

Mushe: Ka yi min zancen da ya kawo ku, ku tashi.

Mouché : Parle-moi de ce qui vous a amené et partez.

Sarkin dogarai: Zance shi ne wannan wanda ya kawo ni. Kuma kana ga matal wannan ɗiya uku ta aihwa abun da za a yi mata kunu ma babu.
Le chef des notables : C’est ce que je viens de te dire. Tu vois cette femme, elle a accouché de triplets, il n’y a même pas de quoi lui faire la bouillie.
Almajirai: I!
Les mendiants : Oui !
Mushe: Wai wa ya ce ta aihu ɗa uku?
Mouché : Qui lui a demandé d’accoucher des triplets ?
Sarkin dogarai: I! To!
Le chef des notables : Ah ! Oui !
Mushe: Ni na ce ta aihu ɗa uku? Ina ruwana mana. Kuma mijin yana ina?
Mouché : Est ce que c’est moi qui lui ai demandé d’accoucher des triplets ? Je m’en fou. Et où est son mari *?*
Sarkin dogarai: Mijin shiriya ya tahi ya barta. Ba ci, ba sha, ya tahi ya shiri ya barta.
Le chef des notables : Son mari est parti et il l’a laissé. Il est parti sans rien lui laisser.
Mushe: Yanzu diba abin da nika tambaya ka, ka ɗauke su ka koma can gidanshi, ka ce mashi akwai dawa ta zo amma ba ni badawa.
Mouché : Ce que je veux de toi maintenant, c’est de les reconduire chef lui, tu lui diras il y a du sorgho mais je refuse de donner. Allez-y, quittez ma maison.
Mushe: Ka ɗauke su ka koma can gidanshi, ka ce mashi akwai dawa, i, amma ban na badawa. Ku tahi ku bar min gidana.
Mouché : Vous retournez chez lui et dites lui qu’il y a le sorgho, oui, mais je réfuse de donner. Sortez de chez moi.
Almajiri: Sadaka!
Le mendiant : L’aumône !
Sarkin dogarai: To!
Le chef des notables : D’accord !
Mushe: Kai kanka. Ka koma can gidanshi ka ce akwai dawa ban badawa, an, ban na badawa.
Mouché : Ta tête. Tu retournes chez lui et dit lui qu’il y a le sorgho je refuse de donner, oui je ne donne pas.
Almajiri: Mushe!

Les mendiants : Mouchés !

Mushe: Kan ga ka koma ta can wurin ka ji ko? Ka ce akwai dawa amman ban na badawa.

Mouché : Tu vois, retourne làbas tu as entendu ? Dis lui que j'ai du sorgho mais je ne donne pas.

Sarkin dogarai: To!

Le chef des notables : D'accord !

Mushe: Ta yaya za ya turo mutane ha gidana? Ku tashi! Ku barmin gidana. E ! Ku tashi. « C'est quelle manière ça? »

Mouché : Comment va-il m'envoyer des gens jusqu'à la maison ? Levez vous ! Quitter ma maison ! Oui ! Levez vous ! C'est quelle manière ça ?

Ɗan caram: Kai sarkin dogarai!

Dan tcharame : Et toi chef des notables !

Sarkin dogarai: Ranka ya daɗe!

Le chef des notables : Que Dieu prolonge votre vie !

Ɗan caram: Amshi ka samu ka sai masu wani abu, ha mu ga abin da Allah ya yi.

Dan tcharame : Tiens, achètes leur quelque chose en attendant de voir ce que Dieu va faire.

Sarkin dogarai: To shi kenan, to shi kenan.

Le chef des notables : Ça ne fait rein, ça ne fait rien.

Ɗan caram: E!

Dan tcharame : Oui !

Sarkin dogarai: Mu je mu. Mu je. A'a!

Le chef des notables : On y va ! On y va ! Non !

Mushe: Ha gida a zo a dinga damun ka kullum sahiya da marece. «Je peux même rester à la maison ». Haka ne kullum. Mushe mun zo a ba mu dawa taimako, Mushe mun zo a ba mu kaza-kaza. Wai ni na yi dubara na ce in zo nan gida in yi aiki yanzu kuma ba su ban lahiya ba, ha gidana? «Vous vous rendez compte? »

Mouché : On vient matin et soir jusqu'à la maison pour te déranger. Je ne peux même pas rester à la maison. C'est comme ça chaque jour. Mouché nous sommes venus chercher du sorgho, Mouché il faut nous donner ceci, cela. J'ai pris le soin de me retirer à la maison pour travailler et même ici je ne suis pas épargné. Vous vous rendez compte ?

Ɗan caram: Kai?

Dan tcharame : Et toi ?

Mushe: Mine ne?

Mouché : C'est quoi ?

Ɗan caram: Wai kai wannan abun da ka yi da ka nuna ma jama'a, gani kake abun alheri ne kake buɗa ma kanka? Na ɗaya hwa kai kuri kake da kai ɗan sarki garin nan ne.

Dan tcharame : Eh, toi ce que tu viens de faire tu crois que c'est un honneur pour toi ? Premièrement tu te vantes d'être un prince de ce village.

Mushe: E, oui «prince des princes » ba.

Mouché : Ah ! Oui, je suis le prince des princes.

Ɗan caram: Kuma wai tammaha kake wai ko yanzu, ko yanzu…

Dan Tcarame : Et tu penses que même maintenant, même maintenant…

Mushe: E!

Mouché : Oui !

Ɗan caram: Wai za ka hawan gadon gidan nan?

Dan tcharame : Et tu penses que tu seras élu comme chef de ce village ?

Mushe: Ba wai tammaha ba ce wannan, ta tabbata, sarauta ta tabbata.

Mouché : Ce n'est pas une pensée, c'est une confirmation.

Ɗan caram: Yo, da wannan gwargwadon da kake, da wannan abubuwan da kake nunawa akwai tallakan, akwai tallakan, da zai goyuwa bayanka ya ce kai yau zaka zama sarkinshi.

Dan tcharame : Avec ton mauvais caractère et ce que tu montres, penses-tu qu'il y a quelqu'un de ce village, il y a quelqu'un qui sera avec toi pour que toi sois son chef ?

Mushe: Ko ba su goyu ba, ko ba su goyu ba, saurata ta zan tabbat.

Mouché : Qu'ils soient avec moi ou pas je serai bel et bien élu.

Ɗan caram: Hum! Wannan dai gayi kake.

Dan Tcharame : Hum!  Tu parles seulement.

Mushe: Na gayi.

Mouché : Je le dis.

Kallamu: A bar zancen wannan.

Kallamou : Laissez tomber.

Ɗan caram: Mutumen banza, mutamen wohi.

Dan tcharame : Tu es un vaurien, tu es un vaurien.

Mushe: Kai ne mutunen wohi.

Mouché : C'est toi le vaurien.

Dan caram: Gwamnati ta aza ku bisa…

Dan tcharame : Le gouvernement vous a placé…

Mushe : «Parce que personne n'est capable, parce que personne n'est capable. »

Mouché : Parce que personne n'est capable, parce que personne n'est capable.

Ɗan caram: Shi ne kake gwadawa wannan? Ƙarya kake wallahi. Wannan shi ne capable? Ɓarayin banza, ɓarin wohi.

Dan tcharame : C'est ça que tu montres ? Tu es un menteur, je le jure. C'est ça être capable ? Vous n'êtes que des voleurs, espèce de voleurs.

Mushe: Kai ne barawo.

Mouché : C'est toi le voleur.

Ɗan caram: Kai yanzu inda gwamnati ta san da abin da kake, billahillazi nine daga gare ni ka ƙare.

Dan tcharame : Toi là si l'état est au courant de ce que tu fais, je te le jure que je vais finir avec toi.

Mushe: Tahi ka gaya ma gwamnati, tahi ka gaya mashi.

Mouché : Va informer le gouvernement, vas-y.

Ɗan caram: Dama na gaya maka, dama ina jiran ka.

Dan tcharame : Je te l'ai dit, je t'attends au tournant.

Mushe: Kana jira na? Munahikin banza, munahikin wohi.

Mouché : Tu m'attends au tournant ? Regarde moi cet hypocrite, espèce d'hypocrite.

*Mushe da Ɗan caram suka fara kokowa, Kallamu yana rabon su.*

*Mouché et Dan tcharame commencent à se battre, Kallamou intervient pour les séparer.*

Kallamu: Saurara dai ban san ba abun da yake kawo wannan abun ba, muna tare sahiya, marece kullun muna tare. Mine ne sabada abu ɗan kaɗan ku tashi kuna ɓata rai?

Kallamou : Ecoutez mais je ne sais pas ce qui se passe entre vous, chaque jour nous sommes ensemble, matin, soir. Pourquoi à cause de quelque chose de rien du tout vous vous querellez ?

Mushe : « Non ! Non ! »

Mouché : Non ! Non !

Kallamu: In dai ba wani abu ke tsakaninku ba mine ne wannan abun?

Kallamou : C'est quoi ça ? Sauf s'il y a quelque chose entre vous.

Mushe: « Non! »Don kai baka san ba « situation » ɗin ba ne. Bari ganin komi a nan, « je connais bien sa position ». Abokin maina Shaho ne.

Mouché : Non ! C'est parce que tu n'es pas au courant de la situation. Ne le vois pas ainsi, je connais bien sa position. C'est l'ami da « maina Chafo. »

Kallamu: Maina Shaho?

Kallamou : Maina Shafo ?

Mushe: « C'est son bras droit ». To da yake shi ma maina Shaho sarauta yake nema yake turo shi gidan Mushe yaga abin da nake yi.

Mouché : C'est son bras droit. Tu vois maina Chafo est aussi candidat c'est pourquoi il l'envoie chez moi pour m'espionner.

Kallamu: Ɗan rahoto kenan?

Kallamou : Donc c'est un espion ?

Mushe: Ƙwarai da gaske. Ya ga irin abin da nake yi a tai can a sare ni wajen manya. Ka ji abin da ya kai. Bari kallan shi nan, ba mutanen kirki ba ne, Allah. Du inda na shiga yana bayana, Allah.

Mouché : Bien sur ! Qu'il voie ce que je fais pour pouvoir me salir auprès de nos chefs. Ne le vois pas ainsi, il ne vaut rien, au nom de Dieu. Partout où je passe il me suit, au nom de Dieu.

Kallamu: To ka san ko da na yi lalata.

Kallamou : Tu sais j'allais dire quelque chose de mauvais.

Mushe: To?

Mouché : Ah bon ?

Kallamu: Dan na so in tada wani zance gabanshi.

Kallamou : Parce que j'ai voulu parler de quelque chose devant lui.

Mushe: Unhum?

Mouché : Ah oui ?

Kallamu: Lalle da na hwaɗe shi da haraka ta lalace.

Kallamou : Certe si je l'avais dis j'allais tout gacher.

Mushe: Zance wane iri?

Mouché : De quoi veux-tu parler ?

Kallamu: Ka san dawakina na suka?

Kallamou : Tu sais que j'ai des chevaux de course ?

Mushe: Umhum!

Mouché : Oui !

Kallamu: To dawa ta ƙare.

Kallamou : Le sorgho est terminé.

Mushe: Assha!

Mouché : Ce n'est pas possible !

Kallamu: Abun da ya sa na zo don in tambaye ka ko na samu buhu biyal haka. In ɗan kai masu kahin kwana biyu.

Kallamou : La raison pour laquelle je suis là, c'est pour te demander si je peux avoir cinq sacs comme ça. Je veux leur amener en attendant.

Mushe *(Ya yi ƴar dariya):* Wannan « ce n'est pas un problème ». Tsakanina da kai ai ba ta kai ba wani roƙo.

Mouché *(Fait un sourire)*: Ça ce n'est pas un problème. Entre nous tu n'as pas à quemender.

Kallamu: Aha!

Kallamou : Ah oui !

Mushe: Dawa koda wane lokaci in dan buhu biyu, buhu uku « pour tes chevaux toi aussi » ko ba ni nan in ka zo ka iske madame ce a baka. Ka san abin zakuwa ya kai « en pagaille ». Kuma ni yadda na ga dama ne nike, ba wani « contrôle » a da kwai ba.

Mouché : Pour le sorgho à n'importe quel moment pour deux sacs ou trois pour tes chevaux toi aussi même à mon absence tu peux venir demander à madame. Ça arrive en pagaille. Je fais ce que je veux avec, c'est sans contrôle.

Kallamu: Amma wanga abun tsoro ne kenan?

Kallamou : Mais cet homme est à craindre ?

Mushe: A'a! Kai dai ka yi dubara da ba ka faɗi ba gaban shi.

Mouché : Non ! Tu as bien fait de ne pas parler devant lui.

Kallamu: Amman wanga abun tsoro ne.

Kallamou : Mais cet homme est à craindre?

Mushe: A'a, kai dai ka yi dubara da ba ka gaya ba gabanshi. To lalle sai ya tai wurin mayan ya sare ni haka, a ce ai Mushe yana mine ne da mine ne. « Tu as très bien fait ». Tunda ba ka

gayi ba gabanshi. Kuma dawa koda wane lokaci in kana so, ko ba ka zo da kanka ba ka turo yaro ya zo.

Mouché : Non! Tu as bien fait de ne pas parler devant lui. Il est capable de me salir auprès de mes chefs, pour dire que je fais ceci je fais cela. Tu as très bien fait. Si tu as besoin du sorgho même si tu n'as pas eu le temps de venir, tu envoies un enfant à tout moment.

Kallamu: Da marice ni turo yara.

Kallamou : Je vais envoyer les enfants ce soir.

Mushe: Ɗan caram, ko ina zagina yake. Ka san Hajiya wannan?

Mouché : Dan tcharame il m'insulte partout où il passe. Tu connais cette Hadjia ?

Kallamu: Na san Hadjia.

Kallamou : Je connais Hadjia.

Mushe: "La même" dai.

Mouché : La même Hadjia.

Kallamu: Um!

Kallamou : Oui !

Mushe: To, can ne nika zuwa « pour d'autres choses. L'autre jour » sai ina jin ƙaras, ƙaras, salama alaikum! Hajiya nanan? Sai na leƙa. Ina kwance bisa gadonta ina ji. Wai gashi nan. Na yi mamakin abin da ya zo biɗa. Ashe bayana yake ya ga abin da nike bata kuma ya tai ya gaya masu. «Non son problème est reglé en tout cas ». Du ra da aka ce an yi sarauta an ƙare daga ƙasa ma hidda shi zan yi Allah. Hidda shi zan yi Allah na ce ma.

Mouché : Donc c'est là-bas que je vais pour d'autres choses. L'autre jour j'enttendais le bruit de pas krass ! Krass ! » « Que la paix soit avec vous ! », Hadjia est là ? J'ai jeté un coup d'œil. J'étais couché sur son lit, j'ai entendu. Le voilà. Je me demende ce qu'il est venu chercher. Il me suit pour voir ce que je lui donne pour qu'il aille dire à mes supérieurs. Non ! Son problème est reglé en tout cas. Quand je serai le chef de ce village je vais le chasser du pays au nom de Dieu. Je te le dis je vais l'expulser du pays.

Kallamu: A, wannan abun gudu ne.

Kallamou : Mais celui là il faut se méfier de lui.

*Hajiya da jikka rataye ga kafaɗa ta shigo gidan Mushe tana buga ƙofa.*

*Hadjia portant son sac fait son entrée chez Mouché et tape à la porte.*

Mushe: Wai ko Hajiya ce yalla?

Mouché : Peut être que c'est Hadjia ?

Kallamu: To wa ya sani?

Kallamou : Qui sait ?

Mushe: A'a, ita ce da kanta, ita ce da kanta.

Mouché : Ah, c'est elle même, c'est elle même.

Kallamu: Ah, Hajiya!

Kallamou : Ah, Hadjia !

Mushe *(Yana dariya)*: Hajiya sannu da zuwa. Sannu-sannu. Yaya? « Ça va » ko? Zamna mana, zamna.

Mouché *(En souriant)* : Bienvenue Hadjia. Bon arrivée. C'est comment ? Ça va ? Prends place, assoies-toi.

Kallamu *(Ya tashi za ya fita):* To! Bari in tashi in tahi.

Kallamou *(Se lève pour partir) :* Bon, je vais partir.

Mushe: A' a!

Mouché : Non !

Kallamu: Son nike in turo yaron ya zo tun da wuri, sabada in na turo shi sai in tai in shiga harakata. Ko ƙaƙa ka gani?

Kallamou : Je veux envoyer l'enfant pour qu'il vienne un peu tôt, parce que j'ai d'autres choses à faire. Où bien que penses-tu?

Mushe: Dan na ce ka yi hira da Hajiya?

Mouché : Parce que je voudrai que tu restes causer avec Hadjia ?

Hajiya: Dan ya gane ni za ya tahiya.

Hadjia : C'est à cause de moi qu'il va partir.

Kallamu: A'a; ba haka ba ne Hajiya! Ko da marece ina dawowa.

Kallamou : Non ! Non ! Hadjia ce n'est pas à cause de ça. Je reviens le soir même.

Mushe: "C'est ça"!

Mouché : C'est ça !

Kallamu: Amma ka san yanzu in barka ka ida aikinka.

Kallamou : Tu sais maintenant je te laisse finir ton travail.

Mushe: Wai, wai! To"d'accord". Hajiya muna lahiya? Na yi kwana biyu ban gewaya wajen naki ba "parce que" aiki ya yi man yawa. "Parce que" motoci suka zo suka kawo abun

taimakon nan na rarrabawa, na aika “adjoint” nau guda, ni kuma na gewaya na bada shiya. Sai ki yi mun « excusez » dan ɗan kwanan nan biyu. Na san yanzu da kin ɓata ranki.

Mouché : Ok ! D’accord ! Hadjia tu vas bien ? Ça fait lontemps que je ne suis pas allé chez toi, parce que j’ai trop de travail. Parce que j’ai reçu beaucoup de voitures qui ont amené du sorgho, donc j’ai envoyé mon adjoint faire la distribution d’une part et moi aussi j’ai fait le tour pour donner le reste. Je m’excuse pour les deux jours. Je sais bien que tu es fachée.

Hajiya: Amman da ko kana cikin aikin kake bari kana tahiya ko?

Hadjia : Mais avant tu laisses ton travail pour aller chez moi non ?

Mushe: I, to Hajiya na yanzu ya zama babba ne shi ma. Ko ba haka ba?

Mouché : C’est que maintenant le travail est plus prèoccupant. Où bien ce n’est pas ça ?

Hajiya: Ba wani babba, indai an sake wuri ai ƙwanda a gaya muna ko?

Hadjia : Il n’y a pas de prèoccupation, si tu as changé d’endroit il faut nous le dire c’est mieux.

Mushe: Ni? In sake wuri Hajiya haba? Yanzu ko wani ya zaka ya ce maki Hajiya Mushe ya sake wuri kin yarda? Wane ni?

Mouché : Moi ? Changer d’endroit ? Même si quelqu’un te dit Hadjia Mouché a changé d’endroit tu vas le croire ? C’est plus fort que moi.

Hajiya: Don mi ba na yarda ba?

Hadjia : Pourquoi ne pas le croire ?

Mushe: Haba Hajiya don Allah bari ɓata ranki, ki yi mini dariya in ji daɗi. Da yau ma na yi niyya in tai in gan ki, Allah ko. Na san dan zancen rabon ga na da ni yi shi ne du ya ɓata miki rai, ko mine ne? Iye?

Mouché : Pardon Hadjia, faut pas te fâcher, fais moi un sourire, ça va me reconforter. Au nom de Dieu même aujourd’hui j’ai l’intention d’aller te voir. Je sais que c’est parce que je t’ai parlé de la distribution que tu es fachée. Où bien c’est quoi ?

Hajiya: Yau, mu ina namu rabon?

Hadjia : Alors, où est notre part ?

Mushe: Rabo da aka yi kin ga na hidda buhu uku na dawa, na hidda buhu biyu na wake na ce a kai ma Hajiya. Mamudu ne inda ya zo, da sai ya ɗauka ya kai maki.

Mouché : En ce qui concerne la distribution, j’ai enlevé trois sacs de sorgho, deux sacs de haricot. Si Mamoudou vient, il va prendre et t’amener ça.

Hajiya: Yau ni goɗiya ce za ka aika mani buhu uku na wake, na dawa ?

Hadjia : Ok, est-ce-que je suis une jument pour que tu m'envoies trois sacs de haricot, de sorgho ?

Mushe: Hajiya!

Mouché : Hadjia !

Hajiya: Dawa ka ga ina ci.

Hadjia : Tu m'as une fois vu manger du sorgho ?

Mushe: Baki ji ba da kyau, na ce na hidda maki shinkahwa, dabino, madara da sukari, du na hidda na ce a aika maki. Ni, ina ni ina aika miki dawa? Haba!

Mouché : Tu n'as pas bien entendu, j'ai enlevé du riz, des dattes, lait et sucre pour t'envoyer. Moi ? Comment je peux t'envoyer du sorgho ? Toi aussi !

Hajiya: Yaya za ka aika mini Mamudu ni da ba mu daɗi ni da shi?

Hadjia : Comment tu vas m'envoyer Mamoudou puisqu'on ne s'entend pas ?

Mushe: In Mamudu ba ya zuwa, na je ni da kaina in kai miki. Ni dai ki hutadda ranki ya yi daɗi. Dama akwa ina so in aika miki wani ɗan abin nan, sabada ga wanga nan *(Mushe ya sanya wa Hajiya kuɗi cikin jikarta)* sabada ana ɗan anhwani da su, a yi kayan miya. A san kin zo gidan Mushe. Ko ba haka ba? Yauwa! Sai kuma na sanya cikin sakwatin ni da kaina? Ni dai in samu lahiya. Wap! A wap! To, i dariya in gani.

Mouché : Si Mamoudou refuse d'aller, je vais aller moi même t'amener. L'essentiel pour moi, est que tu sois heureuse. Dès lors j'ai voulu t'envoyé quelque chose, donc prend ça *(Mouchémet quelques billets de banque dans le sac de Hadjia)* il faut l'utiliser pour tes condiments. Qu'on sache que tu es venue chez Mouché. Où bien ce n'est pas ça ? Il faut que je le mette dans le sac moi-même ? J'ai besoin de la paix. Wap ! Ah wap ! Souris-moi.

Hajiya *(Ta fashe da dariya)*: Hadda wata wahala.

Hadjiya (*Fait un sourire*) : Tu n'as pas à te fatiguer.

Mushe *(Ya yi dariya)*: Hajiye! A! Hajiye! Yaya « ça va » dai ko?

Mouché *(Fait un sourire):* Hadjiye ! Ah ! Hadjiye ! Ça va bien ?

Hajiya: Na ga ka yi baƙi ha suna nan ne ? Zan yi ƴa miya na ce tsaya dai in nemi mutunen da ya ɓace. Ka dai in yi wahala bai je ba.

Hadjia : J'ai vu que tu as reçu des invités, ils sont là ? J'ai voulu preparé, j'ai dis que je vais chercher le perdu. Il ne faut pas que je me fatigue pour rien.

Mushe: A'a! Ba wahala ba ce. Baƙin da sahe suka huta amma suna komowa in aiki ya tashi na zo tare da su in yi miki « présenter » su. Kin ji ko? Wai, wai haka za a yi.

Mouché : Non ! Ce n'est pas un dérangement. Les invités sont sortis ce matin mais ils vont revenir. Je vais te les présenter à la descente. Tu as entendu ? Oui ! Oui ! On va faire comme ça.

Hajiya: To kuma ina son kan aikin ya tashi "onze heures", ina tsumon ka. Ka je ka, ina neman ka.

Hadjia : Je veux que tu viennes à onze heures avant la descente, je t'attends.

Mushe: A'a! "Onze heures" lokacin aiki ne Hajiya, ƙaƙa nika barin aiki in taho wurinki?

Mouché : Ah ! Non ! Onze heures c'est l'heure du service, comment je vais laisser mon travail pour venir chez toi ?

Hajiya: Yaya lokacin aiki? Kenan ba ka je ba?

Hadjia : Comment l'heure du service ? Donc tu ne viens pas ?

Mushe: A' a! Na je, na je tunda kin ce. « Je viendrai. » Ko ba haka ba? Ni dai in samu lahiya.

Mouché: Non! Je viendrai puisque tu me le demandes. Je viendrai. N'est ce pas? Moi là je cherche la paix.

Hajiya: Ina tsumanka.

Hadjia : Je t'attends.

Mushe: To, "d'accord" *(Hajiya ta tashi za ta tafiya)* tahiya za ki?

Mouché : Ok, d'accord ! *(Hadjiya se lève pour partir)* tu vas partir?

Hajiya: Um!

Hadjia : Oui !

Mushe: To bari in ɗan dahwa miki kaɗan.

Mouché : Donc je t'accompagne un peu.

Mushe: Hajiya ba ni son kina ɓata ranki « puisque vraiment » abun nan… to kama dai wadda ki ce.

Mouché : Hadjia je ne veux pas que tu te faches puisque vraiment ces choses là… comme tu l'as dis.

Hajiya: "Onze heures"ina tsumonka.

Hadjia : Je t'attends à onze heures.

Mushe : To"d'accord"!

Mouché : Ok, d'accord !

*Mushe ya yi ma Hajiya rakiya ya dawo ya zamna.*

*Mouché qui a accompagné Hadjia est de retour*

Mushe: "Putain", kai ikon Allah! *(Mushe ya kira Illo)* Illo!

Mouché : Putain ! Dieu est grand ! *(Mushe appelle Illo)* Illo !

Illo: Mushe!

Illo : Mouché !

Mushe: Za ni huta, e, nan bakin kasuwa. Akwai abokina wannan Katinka…

Mouché : Je vais sortir, oui, juste au marché.  Il y a mon ami là Katinka.

Illo: To!

Illo : D'accord !

Mushe: Zai zo in an jima a hidda buhu uku a ba shi. Ka ji ko?

Mouché : Il va venir tout à l'heure, tu lui donnes trois sacs. Tu as entendu ?

Illo: Na dawa ko na shinkahwa?

Illo : Sacs de riz ou du sorgho ?

Mushe: A'a! Ina kai ka ba shi shinkahwa, dawa na ce ma.

Mouché : J'ai dis du sorgho, pas du riz.

Illo: To!

Illo : D'accord !

Mushe: ji ka da karambani. Allah sa in ga ka ba shi na shinkahwa. Ka ji ka da karambani.

Mouché : Tu te mêles de ce qui ne te regarde pas. Il ne faut pas oser lui donner du riz. De quoi tu te mêles.

Illo: To na ba shi, dawa kaɗai ko?

Illo : D'accord je vais lui donner, le sorgho seulement ?

Mushe: E, buhu uku.

Mouché : Oui, trois sacs.

Illo: To na ba shi.

Illo : D'accord, je vais lui donner.

*Mushe ya fita zuwa kasuwa Illo ya koma cikin gida.*

*Mouché sort pour aller au marché et Illo retourne à l a maison.*

**TABLEAU IV**

*Maina Shaho cikin ɗaki yana wuridin kiran rahunnai* yana jan tabzi yana zane a ƙasa. *Badaru ya shigo cikin ɗakin ya zamna ya amshi addu'a tare da maina Shaho.*

*Maina Chafo seul dans sa chambre faisant du chapelet appellant les djins. Badarou entre et fait les invocations avec Chafo.*

Badaru: Salama alaikum! Bisimila dai.

Badarou : Que la paix de Dieu soit avec vous!

Shaho *(Yana yuridi):* Shigo. Ya mu samu, ya mu samu.

Chafo *(Entrain de faire des invocations) :* Rentre. Dieu assiste moi ! Dieu assiste moi

Badaru**:** Amin!

Badarou : Amen !

Shaho: Allah ka taimake ni sarautal nan a ce da ni ne.

Chafo : Dieu assiste moi pour que je sois élu.

Badaru: Amin! Amin!

Badarou : Amen ! Amein !

Shaho: Allah ka taimake ni!

Chafo : Dieu assiste moi !

Badaru: Amin! Amin!

Badarou : Amen ! Amen !

Shaho: Malam Badaru ka zo? Masha Allah! Lahiya hwa.

Chafo : Malam Badarou tu es arrivé ? C'est très bien ! En bonne santé.

Badaru: To barka dai! Lahiya hwa, lahiya hwa.

Badarou : Donc soit la  bienvenue. Bien ! Bien !

Shaho: Yanzu ka zo kenan?

Chafo : Donc tu viens d'arrivée ?

Badaru: E!

Badarou : Oui !

Shaho: Ina nan ina ƙoƙari. Wallahi!

Chafo : Je suis entrain de faire des efforts. Je le jure.

Badaru: Ai dama da na gani na ce to bari haka ƙare.

Badarou : Oui, quand j'ai vu, j'ai dis que je vais te laisser finir.

Shaho: Muna nan muna ƙoƙari sha'anin sarauta.

Chafo : On est là entrain de faire des efforts pour l'affaire de la chefferie.

Badarou: Ai dan haka nan aka ce gado ƙarhin Allah.

Badarou : Comme on le dit l'héritage est une force de Dieu.

Badaru: E! Haka hwa.

Badarou : Oui ! C'est comme ça.

Shaho: Mutun abun da ka gada ya kamata ka ba shi ƙarhi.

Chafo : l'homme doit considererce qu'il a hérité.

Badaru: Kwarai da gaske!

Badarou : Bien sûr !

Shaho: To yaya za a yi? Haka nan ma na sa aka ɗan shasshahe.

Chafo : Comment doit-on faire ? En tout cas j'ai demandé à ce qu'on arrange ici.

Badaru: Amman ya yi kyau hwa!

Badarou : Mais c'est très joli.

Shaho: To yaya tahiya?

Chafo : Et le voyage ?

Badaru: A'a, tahiya ta yi kyau. Komi da komi na samo.

Badarou : Le voyage s'est bien passé. J'ai tout eu.

Shaho: Masha Allahu!

Shafo : Dieu merci !

Badaru: Wannan tahiya ban taɓa tahiya a Kano mai sa'a irin wannan.

Badarou : Je n'ai jamais fais un voyage chanceux sur Kano comme celui-ci.

Shaho: Madalla!

Chafo : Dieu merci !

Badaru: Wannan abokin naka.

Badarou : Ton ami là !

Shaho: To!

Chafo : Oui !

Badaru: Alhaji Sanusi, kai Allah shi yi mashi albarka.

Badarou : Elhadji Sanoussi, qu'Allah le bénisse.

Shaho: Ikon Allah!

Chafo : Dieu est grand !

Badaru: Kai Allah ya yi mashi albarka, wallahi Allah ya yi mashi albarka. Ai a mota ya ɗauke ni na ce mashi ka ji, ka ji ga abin da Shaho ya ce.

Badarou : Que Dieu le bénisse,  je te le jure que Dieu le bénisse. C'est dans sa voiture qu'il m'a pris et je lui ai fais part de tes désires.

Shaho: Masha Allahu!

Hafo : Très bien !

Badaru: Ya ce i wannan, ranshi ya yi daɗi.

Badarou : Il a dis oui, il était très content.

Shaho: Gaskiya ne!

Chafo : C'est la vérité !

Badaru: Ya ce taho mu tai. Mu je nan, ya ce riga ga irin wannan, ga irin wannan, kowace a ɗinke.

Badarou : Il m'a invité.   Nous avons visité des boutiques, il me dit ce boubou voilà les différents modèles, tous sont cousus.

Shaho: Du an sawo?

Chafo : On a tout acheté ?

Badaru: Du an sawo, suna nan.

Badarou : On a tout acheté, ils sont là.

Shaho: Hadda malun malun?

Chafo : Même le grand boubou royal ?

Badarou: Malun malun ka ga irin wannan, ga irin wannan da wannan gudunmuwashi ce. Wannan Allah ya mashi albarka.

Badarou : Il m'a montré les différents modèles de boubous royals, tu vois ce modèleet celui là c'est son cadeau. Lui là, que Dieu le bénisse !

Shaho: Yaya wurin zumuwa?

Chafo: Et en ce qui concerne le miel ?

Badaru: Zumuwa?

Badarou : Le miel ?

Shaho: E!

Chafo : Oui !

Badaru: Zumuwa, gora wajen huɗu ya cika, ya ce ga shi nan, tare da shi yana tahe shi ma.

Badarou : Le miel ? Il a rempli prèsque quatre gourdes, il viendra aussi avec ses invités.

Shaho: Masha Allahu!

Chafo : Dieu merci !

Badaru: Kai wannan mutum Allah mashi albarka.

Badarou : Cet homme là, que Dieu le bénisse !

Shaho: Ina wannan abun na zamani? Lemu!

Chafo : Et cette chose moderne ? Le jus ?

Badaru: Lemu?

Badarou : Le jus ?

Shaho: I!

Chafo : Oui !

Badaru: To wannan ya ce sai in za su zo. Ya ce gaba ɗaya za ya zo da shi. Dan ca ya yi ana kama gobe za a sarauta a dibi hanyashi.

Badarou : Pour ça, il a dit qu'il faut à son arrivée. Il va venir avec tout. Il a dit qu'il viendra la veille de l'intronisation.

Shaho: E!

Chafo : Oui !

Badaru: Ya ce a dai aika mashi yaro. Da an ce ga shi lokaci ya yi a aika mashi yaro.

Badarou : Il a dit seulement de lui envoyer quelqu'un. Le moment venu il faut lui envoyer quelqu'un.

Shaho: A'a! In dai lokaci ya yi sai a aika mai.

Chafo : Oui ! Le moment venu on va lui envoyer quelqu'un.

Badaru: Amma kaka barshi sai ya yi tsawo.

Badarou : Il ne faut pas prendre du temps.

Shaho: Um! Um!

Chafo : Hum ! Hum !

Badaru: Yo ba ku da labarin komi a nan?

Badarou : Vous n'avez pas les nouvelles d'ici ?

Shaho: A'a! Ina gida, ga aikin da aka ba ni ma neman aljannu, wani ruhwani nike nan ina ta abun ga. Ina ni ina  hutani. Ai ni wajen wannan ina ga a kwana ashirin ma ban ga ba waje ba.

Chafo : Non ! Je suis resté à la maison, voilà le travail qu'on m'a donné, moi qui cherche les esprits. Je ne peux pas sortir. Je n'ai pas mis pieds déhors dépuis prèsque plus de vingt jours.

Badaru: To, inhin!

Badarou : Ok, d'accord !

Shaho: An!

Chafo : Oui !

Badaru: Mu tashi tun da wuri.

Badarou : Il faut qu'on se prépare tôt.

Shaho: Tau!

Chafo : D'accord !

Badaru: Da na biyo a tasha nan birni…

Badarou : Quand je suis passé à l'auto gars à Birni.

Shaho: Tau!

Chafo : Oui !

Badaru: Ina wucewa ana zance, sai na ga an yi shiru ana nuna ni.

Badarou : Quand je passais les gens parlent, en me voyant, ils se sont tus et me doigtent.

Shaho: Ana nuna ka?

Chafo : On te doigte ?

Badaru: Ana nuna ni.

Badarou : Oui ! On me doigte.

Shaho: Sabada mi?

Chafo : Pourquoi ?

Badaru: Dan muna tare mana.

Badarou : Parce que nous sommes ensemble.

Shaho: A, i! Gaskiya ne

Chafo : Oui ! C'est la vérité !

Badaru: Yau wani abu ne? In an gani ai an gan ka.

Badarou : Ce n'est rien ? Si on te voie c'est comme si on me voie.

Shaho: In sha Allahu! Yau!

Chafo : Par la grâce de Dieu ! Mais !

Badaru: To nan na jiwo wa'annan mutanen na tasha…

Badarou : C'est là-bas que j'ai entendu ces gens de l'auto gars…

Shaho: To!

Chafo : Oui !

Badaru: Wa'annan mutanen na tasha, masu zama a nan runhwa ta daga nan arewa mi sunansu ma?

Badarou : Les gens de l'auto gars, ce qui sont sous le hangard qui est au nord comment ils s'appellent même ?

Shaho: Ƴan komite?

Chafo : Les membres du comité ?

Badaru: Ƴan komite. Sai na ji suna cewa ai gobe ne. Gobe za a zowa a yi sarauta Nasarawa. Kana gan, dibi riga wannan,  wajen shiga mota.

Badarou : Les membres du comité. Je les ai entendus dire que c'est demain. L'intronisation aura lieu demain à Nassaraoua. Tu vois,  regarde ce boubou, en rentrant dans le véhicule…

Shaho: Um!

Shafo : Oui !

Badaru: Wani ɗan yaro ya kama mani ko ɗan yanken aljihunnan ne?

Badarou : Un garçon m'a saisi, c'est peut être un voleur ?

Shaho: Su ne, su ne.

Chafo : C'est eux, c'est eux.

Badaru: In!

Badarou : Oui !

Shaho : Su ne.

Chafo : C'est eux.

Badaru: Na ce bari in zaburo in gaya maka.

Badarou : J'ai dis que je vais venir vite t'informer.

Shaho: Gaskiya ne, gobe?

Chafo : C'est la vérité, demain ?

Badaru: Um!  Gobe, gobe. A tasha na ji wannan labarin.

Badarou : Oui ! Demain, demain. C'est à l'auto gars que j'ai eu cette information.

Shaho: Ba zancen ƴan ƙwaya ba ne?

Chafo : Ce n'est pas la parole des drogués ?

Badaru: Kai! Haba, wane irin ƴan ƙwaya? Ina ce maka wurin ƴan komite wa'annan su Alhaji. Ka san du abun da aka yi…

Badarou : Ah non ! Quels drogués encore ? Je te dis auprès des membres du comité les Elhadji. Tu sais, ils sont au courant de tout ce qui se passe même tard dans la nuit...

Shaho: To! Insha Allahu!

Chafo : D'accord ! Par la grâce de Dieu !

Badaru: Cikin dare suke samun labarinshi.

Badarou : Ils recoivent les nouvelles la nuit.

Shaho: To! Insha Allahu!

Chafo : D'accord ! Par la grâce de Dieu !

Badaru: Um! Inda abun da, dubara da ke akwai, ka ji dai ni na gaya maka.

Badarou : Hum ! Je t'ai prévenu, s'il y a quelque chose que tu peux faire, moi je t'ai informé.

Shaho: Yau, ai baka sani ba, dubara yau ni kuma an min zancen dubara.

Shafo : Mais tu ne sais pas, moi j'ai plusieurs astuces.

Badaru**:** Yau wace ka samu?

Badarou : Laquelle as-tu trouvée ?

Shaho: Yanzu, kai ai ina da dubara, ni da na kawo malam gobe da nisa a nan garin.

Chafo : Maintenant tu sais j'ai beaucoup d'astuces moi qui ai invité « malam gobé da nissa »

Badaru: Gobe da nisa wanda na sani?

Badarou : Le « gobé da nissa » que je connais ?

Shaho: Kwananshi arba'in a cikin wannan garin.

Chafo : Il a fait quarente jours dans ce village.

Badaru: Anan garin?

Badarou : Dans ce village ?

Shaho: Insha Allahu!

Chafo : Par la volonté de Dieu !

Badaru: Ikon Allah! Biya maradi kenan. Ashe zancen da ka gaya mani sai da ka yi?

Badarou : Dans ce village ? Dieu est grand ! Ça c'est Biya maradi. Tu as fais ce dont tu m'as parlé.

Shaho: Insha Allah! Bari a kira shi ma ya sama albarka.

Chafo : Par la grâce de Dieu ! On va l'appeler pourqu'il te donne sa bénédiction.

Badaru: I! Lalle ko da na …

Badarou : Oui ! C'est juste, j'allais…

Shaho: Laɓaɓa, Laɓaɓa.

Chafo : Lababa, Lababa.

Badaru: Sakaren yaro kenan ka diba dan Allah riga an mashi ba ya ɗinkewa.

Badarou : Cet enfant est un idiot,  il n'est même pas capable de coudre sa chemise.

Laɓaɓa: Yu!

Lababa : Oui !

Shaho: Ka je gidan malam!

Chafo : Tu vas chez malam !

Laɓaɓa: Tau!

Lababa : D'accord !

Shaho: Malam dai?

Chafo : Le même malam ?

Laɓaɓa: Malam inda na kai kaji jiya?

Lababa : Le marabou chez qui j'ai amené des poulets hier ?

Shaho: Ka je gidan malam inda ka kai kaji. Ka ce mashi abin nan, ya zo maza-maza ina jiran shi.

Chafo : Tu vas chez malam là où tu as amené des poulets hier. Dis lui de venir vite-vite, je l'attends.

Lababa:To!

Lababa : D'accord !

Badaru: Malam gobe da nisa ka ce mashi ya zo.

Badarou : Tu dis à malam gobé da nissa de venir.

*Laɓaɓa ya fita da gudu zuwa kiran malam gobe da nisa.*

*Lababa est sorti en courant pour appeler « malam gobé da nissa ».*

Badaru: Akwai sakaran yaro a nan. Shi irin wa'annan yaran a bar aje su a gida, ba su da hankali.

Badarou : Cet enfant est vraiment un idiot. Ce genre d'enfants on ne les garde pas à la maison, ils ne sont pas normaux.

Shaho: Ai, in na ci sarauta kora su za ni.

Chafo : Je vai les chasser quand je serai élu.

Badaru: Ai gara ka kore so.

Badarou : Vaut mieux les chasser.

Shaho: In!

Chafo : Oui !

Badaru: Dan in ba haka ba, da irin wannan za a ji kunya.

Badarou : Avec ce genre d’enfants on aura honte un jour.

Shaho: Ƙwarai ko, ƙwarai ko

Chafo : Bien sur, bien sur.

Badaru: In!

Badarou : Oui !

Laɓaɓa (*Ya shigo da gudu)* : Biya maradi!

Lababa (*Entre en courant)* : Biya maradi !

Shaho: In!

Chafo : Oui !

Laɓaɓa: Ga shi nan zuwa.

Lababa : Il arrive.

Shaho: Tau, tau, to koma can ƙohwa.

Chafo : D’accord ! D’accord ! Donc retourne à la porte.

Laɓaɓa: To!

Lababa : Ok !

Shaho: Ko an tambaye ni ka ce ban na nan.

Chafo : Même si on me cherche, dis que je ne suis pas là.

Lababa: To!

Lababa : D’accord !

Badaru: Um!  Abin da na ce ka…

Badarou : Oui ! Ce que je te dis…..

Malam gobe da nisa  (*Ya shigo gidan Badaru)* : Salamu alaikun!

Malam gobé da nissa  (*Annonce son arrivée)* : Que la paix soit avec vous !

Badaru: A nan?

Badarou : C’est ici ?

Shaho: Amin alaika salam.

Chafo : Amen à toi de même !

Malam: Biya maradi!

Malam : Biya maradi !

Shaho: Allah gahwatta malam. Allah gahwatta malam! Bisimilla! Bisimilla!

Chafo : Votre Eminence ! Votre Eminence ! Rentre ! Rentre !

Malam: Muna lafiya?

Malam : Vous allez bien ?

Shaho: Barka, lahiya lau!

Chafo : Félicitation, très bien !

Malam: Ina gida? Ina aiki.

Malam : Comment va la famille ? Le travail ?

Shaho: Barka! Aiki Alhamdu Lillahi! Barka sannu-sannu.

Chafo : Félicitation ! Le travail Dieu merci. Félicitation, bien, bien.

Malam: Samari ina gida? Muna lahiya?

Malam : Jeune homme comment vas-tu ? Tu te portes bien ?

Badaru: Lahiya lau. An zo lahiya?

Badarou : Bien ! Vous avez fait un bon voyage ?

Malam: Lahiya hwa.

Malam : Très bien !

Badaru: Barka hwa. Mun yi murna hwa.

Badarou : Félicitation. Nous sommes contents.

Malam gobe da nisa: To madalla!

Malam : Merci

Badaru: Mun yi godiya, wallahi.

Badarou : Nous vous remercions

Malam gobe da nisa: Lahiya hwa.

Malam : Très bien !

Shaho: Shi ne abokin nawa da na aika ya saisayo kayan sarautal.

Chafo : C’est mon ami, c’est lui que j’aie envoyé acheter le matériel pour l’intronisation.

Malam: A! Wanda ya tahi.

Malam : Oui ! Celui qui est parti.

Shaho: Da tun ɗazu za shi tahi na ce ya tsaya ka sa mishi albarka.

Chafo : Il a voulu partir dépuis mais je l'ai arreté pour qu'il ait ta bénédicton.

Malam: To madalla! I, mana *(Ya yi addu'a ya dafa kan Badaru ya tofa masa)* Samari tashi albarka ta shige ka.

Malam : Merci ! Tu as bien fais *(Fait quelques invocations sur la tête de Badarou)* Jeune homme lève toi, tu es béni.

Badaru: To madalla. Zan je in adana kayan nan.

Badarou : Donc merci ! Je vais partir déposer ces affaires.

Shaho: To, to!

Chafo : Ok, ok !

Badaru: Gidan ma ban isa ba.

Badarou : Je ne suis même pas allé à la maison.

Shaho: Ap, ba komi a tai a yi wanka.

Chafo : Il faut aller te laver, donc repose toi bien.

Badaru: In Allah ya yarda. Insha Allahu!

Badarou : Si Dieu le veut bien ! Par la grâce de Dieu !

Malam: Yanzu ina gida yaro ya zo.

Malam : Je suis à la maison quand ton garçon est arrivé.

Shaho: I!

Chafo : Oui !

Malam: Ya ce in zo kana kira na.

Malam : Il m'a dit que tu me cherches.

Shaho: Laɓaɓa ni na aikeya.

Chafo : C'est moi qui l'aie envoyé Lababa.

Shaho: Abun ne ina zamne, ka san wannan abokin nawa da ya zo daga sanyen kaya?

Chafo : Je suis là, tu connais mon ami qui vient de faire les achats ?

Malam: E!

Malam : Oui !

Shaho: Shi ya zo mini da wani labari.

Chafo : C’est lui qui m’est venu avec une nouvelle.

Malam: E!

Malam : Oui !

Shaho: Na aikai sanya kaya, tun sarauta ba ta zo ba. Na ce maza-maza ka je ka sayo, to da ya tafi ya zo yanzu tasha wurin manyan ƴan komite nan…

Chafo : Je l’ai envoyé acheté le matériel pour l’intronisation, je lui ai demandé de faire vite, donc à son retour, arrivée à l’auto gare auprès de ces grands membres du comité…

Malam: E!

Malam : Oui !

Shaho: Sai ya ji suna cewa ai a nan ga shi gobe za a yi sarauta. Gobe za a yi, gobe za a yi. Shi ne mahwarin kenan da ya zo ya gaya mani. To shi ne na ce a kira mani kai.

Chafo : Il les a entendus dire que l’intronisation aura lieu demain. Ça se passera demain, ça se passera demain. C’est pourquoi il est venu m’informé. Donc j’ai demandé à te voir.

Malam: E!

Malam : Oui !

Shaho: Dan ka ji. E, dan ka ji kan lokaci ya yi ka ce ban gaya maka ba.

Chafo : C’est pour que tu sois au courant. Oui, c’est pourque tu sois au courant avant qu’il ne soit tard et que tu ne dises que tu n’es pas informé.

Malam: Biya maradi yaushe aka ce?

Malam : Biya maradi, c’est quand ?

Shaho: Hum!

Chafo : Houm !

Malam gobe da nisa: A’a! Yau ni malam gobe da nisa

Malam : Ah non ! Moi « malam gobé da nissa »

Shaho: Inhum!

Chafo : Ah oui !

Malam *(Ya ɗaga tabzinsa ya nunawa Shaho):* Da wannan kaɗai, wannan ai an riga an gama. Yanzu muke jehwata a cikin samaniya, ta rikita samaniya du gaba ɗaya ta gangama mata komi da komi.

Malam *(Prend ses chapelets et les dirige vers Chafo)* : Mais c’est dejà fini. Nous allons la lancer au ciel, elle va faire trembler le ciel et le ciel lui faira tout.

Shaho: To!

Shaho : Ok !

Malam: Tsaya ka gani. Wai mainawan da kuke …

Malam : Laisse voir. Les autres princes avec lesquels vous…

Shaho: E!

Shafo : Oui !

Malam: Da kuke jayayya da su,

Malam : Avec lesquels vous rivalisez,

Shaho: Jayayya?

Shafo : Rivalité ?

Malam: Ka san su?

Malam : Tu les connais ?

Shaho: A, ƙwarai kwa.

Shafo : Ah, oui bien sur .

Malam: Su wane ne?

Malam : Qui sont-ils ?

Badaru: E, da hwarin dai akwai maina Mushe.

Badarou : Premièrement il y a maina Mouché.

Malam : Kuma hwa?

Malam : Et après ?

Badaru: Kuma da maina Ɓaidu.

Badarou : Il y a aussi maina Baidou.

Malam: Maina Ɓaidu?

Malam : Maina Baidou ?

Badaru: Um!

Badarou : Oui !

Malam *(Malam ya buga ƙasa)* : Wannan tashi ta ƙare.

Malam *(Malam gobé da nissa fait sa consultation)* : C'est fini pour lui.

Badaru: Um!

Badarou : Houm !

Malam: Tashi, taka ƙahwa hagu, danna da ƙarhi.

Malam : Lèves-toi, poses le pied gauche, appuie très fort.

Badaru: Tau!

Badarou : D'accord !

Malam: Murza, murza, murza, murza, murza,  koma zamna.

Malam : Piétine, piétine, piétine, piétine, piétine, va t'assoir.

Badaru: To!

Badarou : D'accord !

Malam: Sun ƙare. Ta su ta ƙare daga nan. Akwai  yaro a gidan?

Malam : C'est fini pour eux. C'est fini pour eux à partir de maintenant.  Il y a un enfant dans cette maison ?

Shaho: Akwai yaro.

Chafo : Il y a un enfant.

Malam: A kira min shi.

Malam : Appelle-le.

Shaho: Laɓaɓa! Laɓaɓa!

Chafo : Lababa ! Lababa !

Laɓaɓa: Ayu!

Lababa : Oui !

Shaho: Ikon Allah!

Chafo : Dieu est grand !

Laɓaɓa: Biya maradi!

Lababa : Biya maradi !

Shaho: Ka bi malam.

Chafo : Tu vas avec malam.

Laɓaɓa: To!

Lababa : Ok !

Shaho: Kuma in yana son wasu ma ka kirayi samarin nan na ƙohwa.

Chafo : Et s'il a besoin d'autres tu fais appelle aux garçons qui sont à la porte.

Laɓaɓa: To!

Lababa : D'accord !

Shaho: Ku je ko akwai wani abun ne ka ji ko?

Chafo : Allez-y même s'il y a quelque chose, tu as entendu ?

Laɓaɓa: E!

Lababa : Oui !

Shaho: Wane mutun.Tunda na take Ɓaidu, na take Mushe da man sauran ɗaya ne. Nine kenan. Na tashi tsaye, na sake wunƙuri za su hawa kaina. Zance an ƙare shi kenan. Nine za ni hawa sarauta. Maina Mushe wai shi ne rabon hatsi.

Shafo : N'importe quoi ! Puisque j'ai marché sur Baidou, j'ai marché sur Mouché, il reste un. Donc c'est moi. Je me suis bien préparé, ils veulent me dépasser. L'histoire est donc finie. Je serai intronisé. Et maina Mouché qui fait la distribution du mil.

Malam: Salamu alaikum!

Malam : Que la paix soit avec vous !

Shaho: Amin alaika wassalam. Ha kun zo?

Chafo : De même que toi. Vous êtes dejà de retour ?

*Malam tare da samari ɗauke da ƙatuwar randa cike da rubutu suka shigo gidan.*

*Malam arrive accompagné des garçons qui transportaient un grand canari rempli d'eau coranisée.*

Malam gobe da nisa: Biya maradi mun dawo.

Malam : Biya maradi nous sommes de retour.

Badaru: Lahiya ƙalau!

Badarou : Très bien !

Malam: Ku rakuɓo nan. A hankali, a hankali. Yauwa! Allah muku albarka samari, ku je gida. Biya maradi!

Malam : Allez-y doucement jeunes gens. Allez-y doucement. Approchez doucement par là, doucement. C'est bien, laissez ça ici. C'est bien ! Que Dieu vous bénisse, retournez à la maison. Biya maradi !

Badaru: Na'am!

Badarou : Oui !

Malam: Leƙa nan ka gani.

Malam : Jette un coup d'oeil ici.

Shaho (*Ya yi rairahe ya duɓe tukunyar) : Na* gani. Allah gahwatta !

Chafo (*Marchant à quatre pattes pour voir le contenu du canari) :* Malam j'ai vu. Votre Eminence !

Malam: Kwana arba'in!

Malam : Quarante jours !

Shaho: Gaskiya ne!

Chafo : C'est ça!

Malam: Wannan tunda na zo…

Malam : Dépuis mon arrivée…

Shaho: E!

Chafo : Oui !

Malam: Ban na komi sai wuridi.

Malam : Je ne fais rien que ça.

Shaho: Hum!

Chafo : Houm !

Malam: Ban na komi sai wuridi. Ai wargi wuri gare shi.

Malam : Je ne fais rien que ça. Il y a un lieu pour le jeu.

Shaho: Insha Allahu!

Chafo : Par la grâce de Dieu !

Malam: Ka san ita duniya kowane dare…

Malam : Tu dois savoir que chaque nuit dans  ce monde…

Shaho: I!

Shafo : Oui !

Malam: Ruhwani dubu saba'in yake kewayata.

Malam : Soixent dix mille esprits tournent autour de lui.

Shaho: Hin!

Chafo : Houm !

Malam: In, insha Allahu!

Malam : Oui, par la grâce de Dieu !

Shaho: Dubu saba'in?

Chafo : Soixente dix mille ?

Malam: Dubu saba'in. Kowane dubu kuma yana da tabzi guda.

Malam : Soixente dix mille. Chaque mille a un tour de chapelet.

Shaho: Allahu akabar!

Chafo : Dieu est grand !

Malam: Ya gangama ilu, ya tattara ilu, ya paka-paka.

Malam : Prononce le nom des esprits.

Shaho: Hum!

Chafo : Houm !

Malam: Sarauta taka ce ko shakka babu.

Malam : Sans crainte tu seras roi.

Shaho: Allahu akabar!

Chafo : Dieu est grand !

Malam: Su ne mayan rahunnai.

Malam : Ce sont eux les grands esprits.

Shaho: Su ne mayan rahunnai?

Chafo : Ce sont eux les grands esprits ?

Shaho: Gaskiya ne!

Chafo : C'est la vérité !

Malam: To yanzu dai da yake gobe sarautai…

Malam : Comme c'est demain l'intronisation…

Shaho: Tau!

Chafo : D'accord !

Malam: Sai ka yi ƙoƙari…

Malam : Tu fais un effort…

Shaho: Tau!

Chafo : D'accord !

Malam: Daga yanzu…

Malam : Dès maintenant…

Shaho: Tau!

Chafo : D'accord !

Malam: Ka hwara sha.

Malam : Tu commences à boire.

Shaho: Tau!

Chafo : D’accord !

Malam: Gobe asuba hwarin ya zamanto wannan rubutu ya ƙare, ka shanye shi.

Malam : D’ici demain à l’aube Il faut que cette potion soit finie, tu boies tout le contenu.

Shaho: To!

Chafo : Ok !

Malam: Sarauta taka ko shakka babu. Kakka yi sauna.

Malam : Sans problème le trône est à toi. Sois sans crainte.

Shaho: Aiki!

Chafo : J’ai à faire !

Malam: Amma kuma akwai wani abu.

Malam : Mais il y a une condition.

Shaho: Um!

Chafo : Oui !

Malam: Ka san aikinmu na malammai…

Malam : Tu sais notre travail de marabout…

Shaho: Um!

Chafo : Oui !

Malam: Ba ya son dauɗa.

Malam : Il n’aime pas la saleté.

Shaho: Haka ne, haka ne.

Chafo : C’est ça, c’est ça.

Malam: E, dan saboda ina so in ka hwara shan shi, ko hitsari ya kamaka, biya maradi ka cije kakka yi shi. Amma sarauta an samu tak, tak, ko shakka babu.

Malam : Oui, puisque je veux que quand tu commences à boire même si tu as envie d’uriner, biya maradi abstiens-toi de le faire. Mais le trône” tac, tac,” sans problème est à toi.

Shaho: To, Malam an ji a shanye.

Chafo : Ok, malam j’ai entendu je vais tout boire.

Malam: E, a yi ƙoƙari a shanye. A yi ƙoƙari.

Malam : Oui, il faut faire un effort pour tout boire. Fait un effort.

Shaho: To na gane.

Chafo : Ok, j’ai compris.

Malam: A yi ƙoƙari.

Malam : Il faut faire un effort.

Shaho: A je masabki.

Chafo : Retournez chez vous.

Malam: Tau!

Malam : D’accord !

Shaho: In, a tai masabki.

Chafo : Oui retourner chez vous.

*Malam ya tashi zuwa gida, Shaho ya marmatso ya ƙara buɗe randa ya duba.*

*Malam se lève pour rentrer. Chafo s’approche et jette encore un coup d’oeil dans le canari.*

Shaho: Kai, wannan ni kaɗai in shanye shi kan gobe? Kuma a ce ka in yi hitsari? Kai?

Chafo : Que je bois ça tout seul d’ici demain ? Et de ne pas uriner ? À bon ?

Badaru *(Badaru ya shigo):* Gahwara dai!

Badarou *(Badarou fait son entrée) :* Excusez-moi !

Shaho: Ka shigo?

Chafo : Tu es de retour ?

Badaru: Na shigo. Bismillahi Rahamani Rahim. Yau ka jiƙa maganin zahin nan ɗazu da na shigo ba ka gaya mani ba.

Badarou : Je suis de retour. Au nom d’Allah. Tu as préparé la décoction, j’etais là tout à l’heure et tu ne m’as pas informé.

Shaho: Ba maganin zahi ba ne.

Chafo : Ce n’est pas une décoction.

Badaru: Ba maganin zahi ba ne?

Badarou : Ce n’est pas une décoction ?

Shaho: Ban ce ma na zo da malam ba?

Chafo : Je ne t’ai pas informé de l’arrivée d’un marabout ?

Badaru: Gobe da nisa ko?

Badarou : « Oui, gobé da nissa ? »

Shaho: To! Ashe shi so yake ni in mutu gobe ta mini nisa.

Chafo : Alors, lui il veut que je meure avant demain.

Badaru: Ikon Allah! Wane irin zance ne wannan?

Badarou : Dieu est grand ! De quoi parles-tu ?

Shaho: Leƙa wannan randa.

Chafo : Jette un coup d'oeil dans ce canari.

Badaru *(Ya tashi ya leƙa randar malam) :* Yau ai rubutu ne ko?

Badarou *(Jette vun coup d'œil dans le canari) :* Mais c'est de l'eau coranisée non ?

Shaho: A cike ko?

Chafo : Et c'est plein non ?

Badaru: I!

Badarou : Oui !

Shaho: To wai in yi ƙoƙari kan gobe da sahe…

Chafo : Donc il faut que je fasse un effort d'ici demain…

Badaru: Um!

Badarou : Oui !

Shaho**:** In shanye wannan rubutun kuma ko hitsari ya kama ni ka in yi.

Chafo : Je dois boire toute cette eau et si même j'ai envie d'uriner de ne pas le faire.

Badaru: Randa guda?

Badarou : Tout le contenu du canari ?

Shaho: Gaba ɗaya wai?

Chafo: Le tout?

Badaru: Ka shanye kakka yi hitsari ?

Badarou : De tout boire sans même uriner ?

Shaho: Sunayen manya rahunnai ne wanda suke yin sarauta, wai su wani paka-paka ilu, tattara ilu, gangama ilu, shamsaya ilu wai wai sune mayan rahunnai. Paka-paka'ilu wai mai pazge ruwan sama. Ai ina? Son yake ni in pazge in mutu kamin gobe ko?

Chafo : Il y a les noms des esprits qui font la chefferie, les grands *(Il les cite),* c'est eux les grands esprits. « Pazga illou » c'est lui qui apporte la pluie en abondance. Je ne sais pas où ? Que je meurs avant demain.

Badaru: A'a!

Badarou : Non !

Shaho: In!

Shaho : Oui !

Badaru: Yanzu hwara sha za ka yi.

Badarou : Tu vas commencer à boire maintenant.

Shaho: Wa? Ni?

Chafo : Qui ? Moi ?

Badaru: Um!

Badarou : Oui !

Shaho: A’a! Ba ni sha. Bana ma hwara ba. Bari ma in kira Laɓaɓa!

Chafo : Je ne commence même pas. Laisse je vais appeler Lababa.

Badaru: Shi dai ashe wannan da nike ganin shi da ƙaton rawani mutanen banza ne haka.

Badarou : L’homme là que je vois avec un grand turban ne vaut rien comme ça.

Shaho: Laɓaɓa! Laɓaɓa!

Chafo : Lababa ! Lababa !

Laɓaɓa: Iwu!

Lababa : Oui !

Badaru: A’a!

Badarou : Non !

Shaho: Ka kirawo waɗanda kuka kawo wannan.

Chafo : Appelle ceux avec qui vous avez amené ça.

Laɓaɓa: E!

Lababa : Oui !

Shaho: Ku ɗauka ku kai can ku ba dawaki.

Chafo : Prenez et donnez aux chevaux.

Badaru: Amma dai duniya ta lalace. Yanzu ba a samun malamman kirki sai wannan ƴan danhwara. Wannan ai danhwara ne.

Badarou : Le monde est gaté. Il n’y a que de faux marabouts. Ça c’est un truandage.

Shaho: Na ce maka yanzu malammai na yanzu, waɗansu dai ban ce mika duka ba waɗansu dai ma gwamma bokaye da su.

Chafo : Je te dis les marabouts de maintenant, quelques uns, je ne dis pas tous, certains parmi eux,  les charlatants valent mieux qu’eux.

Laɓaɓa: Biya maradi, randa hwa mi za mi da ita?

Lababa : Biya maradi, qu'est ce que nous allons faire avec le canari ?

Shaho: Randa kai wa uwaka in tana so ta sha. Mi za a yi da ita? Ka ji ko?

Chafo : Tu amènes à ta mère si elle a besoin. Qu'est ce qu'on va faire avec ? Tu as entendu ?

Badaru: A'a! Ni ai abun ya hi ƙarhina.

Badarou : Non ! C'est plus fort que moi.

Shaho: Bokana bagwari yana nan. Shi zan aika shi zo.

Chafo : Mon charlatan "bagoiri" est là.  Je vais le chercher.

Badaru: Wane bagwarin kuma? Wanda kake mini zancen shi?

Badarou : Quel "bagoiri" encore ? Celui dont tu m'as parlé ?

Shaho: Na gaya ma ba?

Chafo : Je t'ai parlé de lui ?

Badaru: Wanda bai jin hausa?

Badarou : Celui qui ne comprend pas le haussa ?

Shaho: I! Na ce maka an gaba ta ƙiya sai a koma baya. In aikin malam ya gagara ba sai mu yi na boka ba?

Chafo : Oui ! Je t'ai dis si on n'avance pas on recule. Si le travail du marabout est impossible il faut essayer celui du charlatant non ?

Badaru: Lalle biya maradi wani abun sai kai.

Badarou : Biya maradi tu es le seul à faire certaines choses.

Shaho: Da ruhannai yake aiki.

Chafo : Il travaille avec les esprits.

Badaru: Yanzu yana nan?

Badarou : Il est dans ce village maintenant ?

Shaho: Yana garin ai. Kwananshi talatin biyu babu.

Chafo : Il est là, il a fait vingt huit jours ici.

Badaru: Um! Yau ashe an ji jiki? Ikon Allah! Gara da ka gaya mani.

Badarou : Houm ! Donc tu as beaucoup depensé ? Dieu est grand ! Tu as bien fait de m'informer.

Shaho: Tsaya ka ga a kira shi yanzu.  Laɓaɓa! Laɓaɓa!

Chafo : Laisse voir, on va l'appeler tout de suite. Lababa ! Lababa !

Laɓaɓa: Iyu!

Lababa : Oui !

*Laɓaɓa ya zo da fushi ya juye kanshi.*

*Lababa est venu fâcher et tourne sa tête.*

Shaho: Kai wannan wane irin sakaren yaro ne ni jama'a za ai? Kai ni yanzu wannan wandon naka Laɓaɓa mine ne wannan? Um!

Chafo : C'est quel genre d'idiot cet enfant là? Ce pantalon là c'est quoi Lababa ?

Shaho da Badaru: Mi ye?

Chafo et Badarou: Il y a quoi ?

Laɓaɓa: Biya maradi mi ye?

Lababa : Biya maradi c'est quoi ?

Shaho: Jeka ka kirawo mini boka.

Chafo : Vas-y m'appeller le charlatant.

Laɓaɓa: Ina? Inda na kai ɗan bunsuru baƙi?

Lababa : Où ? Là où j'ai amené le bouc noir ?

Badaru: Ka kai toron giwa, tai ka kira mini shi kurum. Haka yake.

Badarou : Tu as amené l'éléphant, vas l'appeller seulement. Il est comme ça.

*Laɓaɓa ya hita da gudu zuwa kiran boka.*

*Lababa sort en courant pour aller chez le charlatan.*

Badaru: Subahani Lillihi, irin wannan yaran ai ba a abun asiri da su.

Badarou : Que Dieu nous préserve ! Ce genre d'enfants on ne fait pas de choses secrètes avec eux.

Shaho: Wannan an ya tai gari ma hwaɗi yake muna wane ne, muna wane ne. Mutumen banza mutumen wohi.

Chafo : Celui là s'il part en ville il va dire que nous faisons ceci cela. Le vaurien.

Laɓaɓa *(YA dawo)* : Ga shi nan zuwa.

Lababa *(De retour) :* Il arrive.

Shaho: To, tahi can ƙohwa ka zamna. In wa ya zo, ko an tambaye ni ce ban ni gidan

Chafo : Ok, vas là-bas à la porte. Dis à tout celui qui me demande que je suis sorti.

Laɓaɓa: To!

Lababa : D'accord !

Shaho: Ban ni gari.

Chafo : Je ne suis pas dans la ville.

Laɓaɓa: To!

Lababa : D'accord !

Shaho: Kowa ka ya shigo gidana. Ban ni nan.

Chafo : Que personne ne rentre chez moi. Je ne suis pas là.

Laɓaɓa: To!

Lababa : D'accord !

Badaru: Ni ma zan koma.

Badarou : Moi même je vais retourner.

Shaho: A'a!

Chafo: Ah non !

Badaru: A'a ! Ka san aljannu su ba mu bin hanya ɗaya ni da su?

Badarou : Non ! Tu sais les esprits et moi nous ne suivons pas le même chemin ?

Shaho: To mu muna bi.

Chafo: Nous nous suivons.

Badaru: Subahani Lillahi!

Badarou : Que Dieu nous en garde !

*Boka ya shigo tare da mataimakinshi, yana gyaggyewaya Shaho da yake zamne saman tabarma yana yi yana karkaɗa wani abu mai ƙara yana wasu maganganu.*

*Le charlatan rentre avec son aide, il tourne autour de Chafo en manipulant sa cloche et en faisant des incantations.*

Shaho: Muna lahiya?

Chafo : Comment vous allez ?

Yaron Boka: Lahiya lau!

Aide charlatan : Bien !

Shaho: Sannunku da zuwa.

Chafo : Soyez la bienvenue !

Yaron Boka: Sannu kadai!

Aide charlatan : Merci !

Shaho: To madalla, madalla. Gaida min shi.

Chafo : C'est bien, c'est bien. Dis lui bonjour de ma part.

Yaron Boka *(Ya yi wasu maganganu da Shaho ba ya iya gane wa)* : Ya amsa. Biya maradi yaron naka ya ce boka ya zo.

Aide charlatan *(Prononce quelques paroles que Chafo ne comprend pas)* : Il a répondu. C'est ton enfant qui est parti appeler le charlatan.

Shaho: I! Ni na aikai.

Chafo : Oui ! C'est moi qui l'ai envoyé.

Yaron Boka: Lahiya?

Aide charlatan : Qu'est ce qui ne va pas ?

Shaho: Yau ca aka yi gobe za a naɗa sarauta a nan Nasarawa.

Chafo : Il parait que l'intronisation aura lieu demain ici à Nassaraoua.

Yaron boka: Gobe?

Aide charlatan : Demain ?

Shaho: E! Shi ko ya zo don a yi wannan sha'anin, duka dama kwana da kwanaki ana yanke mashi shanu yana sha. Ya ce an lokaci ya zo a gaya mishi. Ba sai a gaya mashi ba?

Chafo : Oui ! Il est venu pour ça bien que des jours et des jours il mange les vaches qu'on lui égorge. Il a dis de l'informer au moment venu. C'est normal qu'on l'informe non?

Yaron boka: Daidai ne, bari a gaya mashi.

Aide charlatant : C'est normal, je vais lui dire.

Shaho: To!

Chafo : D'accord !

*Yaron boka ya juwa wajen boka suka yi wasu maganganu da su kaɗai suka san abin da suke cewa, sa'annan ya juwo wajen Shaho don ya gaya mashi abin da bokan ya faɗi.*

*L'aide du charlatan parle au charlatan avec des propos dont eux seuls comprennent. Ensuite il fait l'interprétation à Chafo.*

Yaron boka: Ya ce to ya ji amma zai dubawa kuma a ga abin da ya hi.

Aide charlatan : Il a entendu mais il va essayer de voir ce qu'il y a lieu de faire.

Shaho: Tau!

Chafo : D'accord !

*Boka ya yi wa yaronshi wasu maganganu.*

*Le charlatan parle à son aide.*

Yaron boka: Ya ce zai dubawa cikin wanga abun, inda a da babban aljani Yubana du abin da ya ce kuma ka sani.

Aide charlatan : Il va regarder dans cette chose, là où il y a le grand genie Youbana, tout ce qu'il décide tu le sauras.

Shaho: Ai ni du abin da yake so na yi.

Chafo : Je ferai tout ce qu'il veut.

Yaron boka: To shi kenan.

Aide charlatan : Donc il n'y a pas de problème.

Shaho: E!

Chafo : Oui !

*Boka ya tashi tsaye yana ta yin wasu abubuwa yana wasu maganganun da shi kaɗai ya san abin da suke nuhi. Gaba ɗaya suka tashi suna rawa boka yana kiran Yubana bayan sun ƙare suka zamna kuma suka cigaba da yin zakuɗe-zakuɗe daga zamne.*

*Le charlatan fait des incantations que lui seul comprend. Ensuite ils se mettent tous ensemble à danser, le charlatan prononçant "Youbana" à chaque fois. Aprés ils se mettent assis et commencent à danser.*

Yaron boka: Ya ce ka ga abun an yi sa'a.

Aide charlatan : Tu vois on a de la chance.

Shaho: Um!

Chafo : Oui !

Yaron boka: Ya duba nan Alhamdu lillahi ya ga wani mutun zamne nan cikin wurin nan da rawani.

Aide charlatan : Il a regardé et Dieu merci, il a vu un homme enturbané assis sur cette place.

Shaho: I, yauwa!

Chafo : Oui, très bien !

Yaron boka: Um !

Aide charlatan : Oui !

*Yaron boka da boka suka sake yin irin maganarsu.*

*L'aide charlatan et le charlatan ont repris leurs incantations.*

Yaron boka: Amma hwa akwai abubuwa. Sarauta ta tabbata amma hwa akwai abubuwa

Aide charlatan : Mais il y a des choses à faire. La chefferie c'est sûre mais il y a des choses.

Shaho: Inhun!

Chafo : Et oui !

*Boka da yaronshi suna magana.*

*L'aide charlatan et le charlatan ont repris leurs incantations.*

Yaron boka: Ka ga hwarko an hwara da neman gora giya uku, kai guda, ni guda, shi guda. Suna samuwa?

Aide charlatan : D'abord on va chercher trois gourdes de bière, une pour toi, une pour moi et la troisième pour lui. On peut les avoir ?

Shaho: A samu giya?

Chafo : Avoir de la bière ?

*Boka da yaronsa suna magana.*

*L'aide charkatan et le charlatan ont repris leurs incantations.*

Yaron boka: Kuma sai an nemo ɗan bunsuru.

Aide charlatan : Il faut aussi chercher un bouc.

Shaho: Akwai shi.

Chafo : Il y a dejà ça.

Yaron boka: Shi wannan yankawa za a yi a ba Yubana jinin, mu kuma nama mu ci.

Aide charlatan : On va l'égorger pour donner le sang à Youbana et nous, nous mangeons la viande.

Shaho: Inhun!

Chafo : Et oui !

*Boka ya yi wata babba dariya ya cigaba da abin da yake yi ya juwo wajen yaronsa suka yi magana*

*Le charlatan fait un grand sourir et continu son incantation puis retourne vers son aide et lui prononce quelques paroles.*

Yaron boka: Amma hwa da saura. Du abun da aka gayama in kana iyawa ka hwaɗì, wanda ba ka iyawa ka hwaɗì.

Aide charlatan : Mais ça reste encore. Tout ce qu'on te dit si tu peux tu nous le dis  et ce que tu ne peux pas  tu nous le dis aussi.

Yaron boka: Yanzu wannan mai wuya ne. Ca ya yi in gaya ma, kuma ka gaya muna gaskiya.

Aide charalatan : Maintenant celui là est difficile. Il m'a chargé de te dire, et tu nous dis la vérité.

Shaho: A tau!

Chafo : Ah oui !

Yaron boka: Jaka za a nemowa.

Aide charlatan : Tu vas chercher une ânesse.

Shaho: A'a!

Chafo : Non !

Yaron boka: To madalla. Yanzu abin da ya gaya mani ita jaka in ka nemo ta…

Aide charlatan : Très bien ! Ce qu'il m'a dis si tu arrives à trouver l'ânesse …

Shaho: Tau!

Chafo : Ok !

Yaron boka: Ka ji ko?

Shaho: An!

Chafo : Oui !

Yaron boka: A ɗauki lizzame a aza mata, a ɗauki sirdi a aza mata, sannan kai kuma wannan rawanin na ga kai…

Aide charlatan : Tu as entendu ? On lui pose la selle, on lui attache les mors et après toi ce turban que tu portes…

Shaho: Tau!

Chafo : Ok !

Yaron boka: Sai ka nemi ɗan tisi ka ɗaura, sai ka hau jaka nan, ka nemi inda aka taron, sai ka nihi taron…

Aide charlatan : Tu cherches un morceau de tissu que tu attaches et montes sur l'ânesse, tu vas là où l'intronisation se passe…

Shaho: Tau!

Chafo : Ok !

Yaron boka: Sai ka kama lizzamen nan ka buga bayanta ka hwara" Yubana! Yubana! Yubana!" Kuma ka tahi wurin taron nan…

Aide charlatan : Tu attaches un morceau de tissu et tu montes sur cette ânesse, tu cherches là où se passe la cérémonie, tu tires les mors et tu commences à crier “Youbana! Youbana! Youbana!” Tu vas jusqu’à là où se passe la cérémonie.

Shaho: Tau!

Chafo : D’accord !

Yaron boka: Kuma da ka tahi wurin taron nan sai ka sabka saman jaka ka hidda rawaninka sai a sa ma rawanin sarauta, saurata ta ƙare.

Aide charlatan : Tu descends, tu enlèves ton turban et on te noue le turban de la chefferie, c’est fini.

Shaho: Tau!

Chafo : D’accord !

Yaron boka: Amma ya ce a tambaye ka in kana iyawa.

Aide charlatan : Il veut savoir si tu peux.

Shaho: To wai gaya mishi.

Chafo : Demande-le.

Yaron boka: Tau!

Aide charlatan : D’accord !

Shaho: Da dare zan hawo jakal ko da rana?

Chafo : Je dois monter l’ânesse le jour où la nuit ?

Yaron boka: Tau!

Aide charlatan : D’accord !

*Boka da yaronsa suna magana.*

*L’aide charlatan et le charlatan ont repris leurs incantations.*

Yaron boka: Da rana katankar, da rana katankar.Wane irin dare? An taɓa sarauta da dare? Da rana za ka hawan jaka.

Aide charlatan : En plein jour, en plein jour. Quelle nuit ? Est ce qu’on a une fois fait l’intronisation la nuit ? Tu vas monter sur l’ânesse le jour.

Shaho: To ka ce mashi babu wani abu wanda za a yi sai na hawo jaka?

Chafo : Dis lui il n’y a pas une autre issue, il faut que je monte sur l’ânesse ?

Yaron boka: Tau!

Aide charlatan : D’accord !

*Boka da yaronsa suna magana.*

*L'aide* charlatan *et le charlatan ont repris leurs incantations.*

Yaron boka: Babu wata dubara sai ka hawo jaka, babu wata dubara sai ka hawo jaka. Tashi tsaye!

Aide charlatan : Il n'y a pas une autre issue, il te faut monter sur l'ânesse, il n'y a pas d'autres issues, il te faut monter sur l'ânesse. Lève-toi !

Yaron boka: Tashi tsaye *(Shafo ya tashi)* zo ku haɗu, zo ku haɗu. Matsa can, matsa can. Bukata ta biya *(Boka da yaronshi suna gewayar shi)* bukata ta biya, bukata ta biya.

Aide charlatan : Mets-toi debout (*Chafo se lève)* viens à sa rencontre, viens à sa rencontre. On a eu satisfaction (*Le charlatan et son aide* tournent *autour de lui en faisant des incantations)* on a eu satisfaction, on a eu satisfaction.

*Boka da yaronsa suka fita daga gidan Shafo bayan sun ƙare aikinsu.*

*Après sa consultation Boka et son aide sortent de la maison de Shafo.*

Shaho: Allah ɗebe ma albarka! Bokan banza, bokan wohi. Ca nike wani abin kirki ne ashe bokan banza ne aka kawo. Ɗan kare ya sami yaro mai tsananin wayon tsiya ha ya kusa hwasa min kai ɗan kare.

Chafo : Que Dieu te maudisse ! Mais c'est un vaurien. Je croiyais que c'est quelqu'un de bien qu'on m'a amené, mais c'est un vaurien qu'on m'a amené. Il a eu un adjoint très malin, fils de chienne il a failli me casser la tête.

**TABLEAU V**

*Badaru ya komo gidan Shafo.*

*Badarou revient chez Chafo.*

Badaru: Salamu alaikun! Gahwra dai!

Badarou : Que la paix soit avec vous ! Puis je rentrer ?

Shaho: Sannu da zuwa.

Chafo : Bienvenue !

Badaru: Yauwa, Bismillahi Rahamani Rahim.

Badarou : Très bien ! Au nom Dieu le Clément le Miséricordieux.

Shaho: Anya sha'anin namu ya yiwu?

Chafo : Est ce que notre affaire est réalisable ?

Badaru: Lahiya? Na iso gidan ma nike ji ana tankiya ana ihu. Lahiya dai?

Badarou : Qu'est-ce qui ne va pas ? En m'approchant de chez toi j'ai enttendu des bruits et cris. Qu'est ce qui ne va pas ?

Shaho: Wannan Allah tsine wannan bokan. Ka san abin da ya yi mini shi?

Chafo : Que Dieu maudisse se charlatan. Tu sais ce qu'il m'a fait ?

Badaru: Bokan?

Badarou : Le charlatan ?

Shaho: Ai gara malam da shi.

Chafo : Le marabout est mieux que lui.

Badaru: Ap! Ikon Allah!

Badarou : Oh ! Dieu est grand !

Shaho: Wani sauran abin ba ya hwaɗuwa.

Chafo : Je ne peux pas raconter certaines choses.

Badaru: Inhun ?

Badarou : Ah, oui ?

Shaho: Wannan sha'ani, ɗan gidan nashi da yake ya lalace ya je ƙasassu ya zamna ya lalace ya zama irin su.

Chafo : Cette affaire, ce garçon qui est parti chez eux et a changé, il est devenu comme eux.

Badaru: In!

Badarou : Oui !

Shaho: Ka ji ko? Shi ma a bashi gora giya ɗaya kuma ni aban ɗaya in sha.

Chafo : Tu as entendu ? On lui donne une gourde de bière et moi aussi on me donne une gourde.

Badaru: Subahani lillahi!  Ka yi mi?

Badarou : Que Dieu nous préserve ! Tu fais quoi ?

Shaho: Wai in sha.

Chafo : Que je boive.

Badaru: A 'uzu Billahi!

Badarou : Que Dieu nous en garde !

Shaho: Wai ni na ce in je gaba, da ya yi wuri-wuri ya san sarauta gobe ce sai ca ya yi in nemi wai baƙa jaka

Chafo : Moi qui ai voulu avancer, quand il a cherché et qu'il sait bien que l'intronisation est pour demain donc il me dit de chercher une ânesse noire.

Badaru: A 'uzu Billahi!

Badarou : Que Dieu nous en garde !

Shaho: Dama in na sha giya na koshi.

Chafo : Après avoir bien consommé l'alcool.

Badaru: Um!

Badarou : Oui !

Shaho: Kuma ya ce a nemo ɗan akuwa mai gemu a yanka, wai a ba Yubana jinin su su ci nama.

Chafo : Il dit de chercher un bouc barbu pour donner le sang au genie Youbana et eux ils mangent la viande.

Badaru: Wane ne Yubana kuma?

Badarou : Qui est Youbana encore ?

Shaho: Wani aljaninsu ne. Ka ji ko?

Chafo : C'est leur genie.

Badaru: Um!

Badarou : Oui !

Shaho: Na ce masa to na ji wannan. Sai ca ya yi to yanzu abin da ake so da ka nemo baƙa jaka…

Chafo : J'ai dit que j'ai entendu. Et il dit ce qu'on veut maintenant, dès que tu trouves l'ânesse noire…

Badaru: Tau!

Badarou : D'accord !

Shaho: Ka ɗaura mata sirdi da lizzami.

Chafo : Tu lui montes une selle et tu lui attaches les mors.

Badaru: Ikon Allah!

Badarou : Dieu est grand !

Shaho: Kai ko ka yi ɗan rawani wai in hudda wa'annan kayan in sa kaya na wohi irin nasu, in hito hili kuma in hawo wannan baƙa jaka in nuhi inda ake sarauta ina hwaɗin « Yubana,

Yubana, Yubana ». Wai in na je za a hudda wannan ɗan rawanin kuma a sabkeni daga jaka za a min sarauta ni ne sarki.

Chafo : Et moi j'enlève mes habits et je mets des habits semblables aux leurs, je mets un turbant et je sors en plublic et je monte sur cette ânesse noire je fonce là où se passe l'intronisation en criant « Youbana ! Youbana ! Youbana ! » Dès que j'arrive on va m'enlever ce turbant et on me fait decendre de l'ânesse et je deviens roi.

Badaru: A'uzu Billahi mina shaiɗani razim! Kai za ka hwan baƙa jakal?

Badarou : Que Dieu nous en garde ! C'est toi qui va monter sur l'ânesse noire ?

Shaho: Wai ni ne da rana, inda da dare ne.

Chafo : C'est moi qui vais le faire le jour, si c'est au moins la nuit.

Badaru: Yau in da dare ne sai ka hawo?

Badarou : Et si c'est la nuit, tu vas monter ?

Shaho: A, yo dan sarauta.

Chafo : Mais oui pour être roi.

Badaru: Ashe da rana ma ka hawo.

Badarou : Donc même le jour tu peux monter.

Shaho: A yau to.

Chafo : Ah mais oui.

Badaru: Yau kuma ka riƙa cewa mi?

Badarou : Et puis tu cris en disant quoi ?

Shaho: Yubana, Yubana?

Chafo: Youbana, Youbana !

Badaru: Da rana?

Badarou : En plein jour ?

Shaho: A'a to!

Chafo : Ah oui !

Badaru: A'a! Yau sun ƙare ma sarauta.

Badarou : Non ! Ils t'ont déja élu.

Shaho: Um!

Chafo : Oui !

Badaru: A'a!  Diba mana ka gani, lattijo kama kai, a ce ya hawo jaka yana gaba yana baya; yana hwaɗin Yubana, Yubana, yau ba an ma sarkin shaggu ba kenan? Haba mana wannan abun ba mai kawo alheri ba ne. Ka gane ko?

Badarou : Non ! Maintenant regarde, on demande à un sage comme toi de monter sur une ânesse en faisant des va-et-vients et en criant Youbana Youbana, donc on t'a intronisé le roi des imbéciles non ?  Toi aussi tu penses que c'est une bonne chose pour nous. Tu as compris non ?

Shaho: Um!

Chafo : Oui !

Badaru: Ka ga can ma ina gaya maka ina cewa malam makaho mu rinka waiwaya shi.

Badarou : Tu vois dès lors je te disais qu'il faut que nous consultons de temps en temps « malam makafo »

Shaho: Gaskiya ne!

Chafo : C'est la vérité !

Badaru: Kake cewa gobe da nisa, ga shi ya zo yi mumu nisan dan Allah.

Badarou : Tu dis "gobe da nisa", il est venu s'éloingner de nous.

Shaho: Allah wadan naka ya lalace, wannan ai shaƙiyanci ne. Allah wadan boka bagwari.

Chafo : Que Dieu maudisse les mauvaises personnes, c'est des imbécilités. Que Dieu maudisse le charlatan « bagoiri »

Badaru : Yanzu tashi za ka yi  tunda dai amana ce ubanka ya bada mu gare shi, tashi mu tai mu tarda malam makaho.

Badarou : Maintenant tu viens on va chez «malam makafo » puisque c'est ton père qui nous a confiés à lui, viens on va aller le trouver.

Shaho: Ai sai wajen malam makaho.

Chafo : Donc oui il faut aller chez «malam makafo »

Badaru: Mu ce mun saki hanya amma ya maido mu ga hanya.

Badarou : Nous allons lui dire que nous nous sommes égarés de nous ramener sur le droit chemin.

Shaho: Tashi mu tai!

Chafo : On y va !

Badaru: Haka nan za mu yi amma Allah tsine ma boka bagwari.

Badarou : On va faire comme ça mais que Dieu maudisse le charlatan « bagoiri ».

Shaho: Allah wadan boka.

Chafo : Que Dieu maudisse le charlatan.

**TABLEAU VI**

*Ranar naɗin sarauta ta zo. Filin sarki ya cika da mutane maza da mata. Ana jiran purepe da kumandan su bayyana sunan wanda Allah ya ba nasara. Mainawa suna tsaitsaye kowane daga cikin su yana tsammanin shi ne za a zaɓa. Makaɗan sarki suna ta yin kiɗa da bushe-bushen algaita.* Sekretair jeneral *ya tashi wuza yin jawabin buɗe taron bayan da manyan baƙin suka zo suka zamna.*

*C'est le jour de l'intronisation. La place du chef est pleine de monde hommes et femmes. On attend à ce que le Préfet et le Sous-préfet nomment celui à qui Dieu a donné la chance d'être élu. Tous les princes étaient là chacun pense qu'il est l'heureux élu. Les griots du roi font leur tambour. Le sécretaire général se lève pour prononcer le discours d'ouverture.*

Maroƙi: A saurara, ku saurara, a saurara, jama' a a saurara!

Le griot : Ecoutez, écoutez, votre attention, écoutez !

*An sake cigaba da kiɗi da busa algaita.*

*L'animation continue.*

Sekretair jeneral: Mai girma « préfet », mai girma « sous-préfet, monsieur le député national », e jama'a mutanen Nasarawa salamu alaikum.

Sécretaire général : Monsieur le préfet, monsieur le sous-préfet, monsieur le député national population da Nassaraoua que la paix soit avec vous.

Maroƙi: Amin!

Le griot : Amen !

Sekretair jeneral: Da sunana ni, sekretair jeneral na nan Nasarawa, da sunanku ku duka gaba ɗaya, ina yi wa mai girma purepe maraba da zuwa garinmu Nasarawa.

Sécretaire général : A mon nom, moi le sécretaire général de Nassaraoua, et à votre nom tous, je souhaite la bienvenue à monsieur le préfet, bonne arrivée à Nassaraoua.

Maroƙi: Amin!

Le griot : Amen !

Sekretair jeneral: Ba zan yi wani dogon diskur ba saboda kun san rana ta yi. « Seulement », ina son in yi « profiter » tunda « occasion » ta samu mu kai godiyamu wajen mai girma « Préfet » na taimakon da akai muna ha kullun.

Le sécretaire général : Je ne serai pas long puisqu'il fait déjà tard, seulement je veux profiter de cette occcasion pour remercier monsieur le préfet pour l'aide qu'il nous envoie toujours.

Maroƙi: Amin!

Le griot : Amen !

*Mutane suka amsa da amin tare da bushe-bushen algaita. Mushe ya cigaba da jawabi.*

*L'animation continue. Mouché poursuit son discours.*

Sekretair jeneral: Daga nan kuma jama'a sai in ce maku assalama alaikum.

Le sécretaire général : Sur ce, je vous dis que la paix soit avec vous.

Maroƙi: Amin! Amin ya Allah!

Le griot : Amen ! Amen ! Par la grâce de Dieu !

*Bayan Mushe ya ƙare jawabinsa aka cigaba da kiɗe-kiɗe da bushe-bushen algaita. Kumandan ya shigo filin don yin nasa jawabin.*

*Après le discours de Mouché, l'animation a continué. Le commandant fait son entrée pour faire son discours.*

Maroƙi: A saurara! A saurara, kai kumandan za shi magana. A saurara!

Le griot : Ecoutez ! Écoutez ! Le commandant va prendre la parole. Écoutez !

Kumandan: Jama'a maza da mata mutanen nasarawa salama alaikum.

Le commandant : Population de Nassaraoua, hommes et femmes que la paix soit avec vous.

*Aka buga ganga aka yi taɓi tare da amsa salamar kumandan.*

*Animation et le commandant continue son discours.*

Maroƙi: Amin!

Le griot : Amen !

Kumandan: Ina so in gwada maku hwarin cikina ƙwarai da jiran da kuka mumu a nan, na ji daɗi ƙwarai.

Le commandant : Je suis très heureux de l'accueil que vous nous avez reservé ici, je suis très content.

*Aka buga ganga kuma suka amsa da amin. Sai kumandan ya cigaba da jawabinsa.*

*Animation. Le commandant continue son discours.*

Kumandan: Haka kuma ga shi Allah ya kawo mu rana da na ce maku za mu zo tare da mai girma Purepe sabada a naɗa saban sarki.

Le commandant : Nous voilà aujourd'hui comme prévu, le jour où je vous ai dis que nous allons venir avec Préfet pour l'intronisation du nouveau roi.

Maroƙi: Gaskiya ne!

Le griot : C'est juste !

Kumandan: Ba zan ja dogon hira ba, sai in ba « monsieur le Préfet » wuri sabada ya gaya maku abin da ya kawo mu. Assalamu alaikum.

Le commandant : Sans trop tarder, je laisse la parole à monsieur le Préfet pour vous dire ce qui nous à amener. Que la paix soit avec vous !

*Ana yi ta kiɗa  da busa kafin Purepe ya ɗauki magana. Purepe ya shigo filin don yin jawabi*

*L'animation continue. Le Préfet fait son entrée pour faire son discours*

Maroƙi: A saurara! A saurara! Purepe za ya yi magana da kansa. A saurara!

Le griot : Ecoutez ! Écoutez ! Monsieor le Préfet va prendre la parole. Écoutez !

Purepe *(Ba ya jin hausa da kyau):* Zama'a mutane nasarawa mace da namizi, salama alaikum.

Le préfet *(Ne parle pas pas bien la langue) :* Population de Nassaraoua hommes et femmes que la paix soit avec vous.

*Jama'a suka taɓa kuma aka buga ganga tare da cewa amin.*

*L'animation continue.*

Purepe: E, kafin in yi wanga magana, ina tambaye ku gafara, sabada kun san hausana, bai shi da ƙarfi.

Le préfe t: Oui, avant de continuer je vous demande de m'excuser parceque je ne parle pas bien la langue.

*Jama'a suka taɓa kuma aka buga ganga*

*L'animation continue.*

Purepe: Bayan hakanan kuma wannan rana da anka ce za mu zo mu, yau ga mu, mun zo nan dan mu naɗe maku sabon sarki.

Préfet : Nous sommes venus comme prévu, nous sommes là pour introniser le nouveau roi.

Maroƙi: Mai rabo ya samu, mai rabo ya samu.

Le griot : Le chanceux est déjà choisi, le chanceux est déjà choisi.

*Jama'a suka taɓa kuma aka buga ganga aka busa algaita.*

*L'animation continue.*

Purepe: Kafin mu naɗe maku sabon sarki ina meku gaisuwa na sarki wancen da ya rasu, Allah ya zikan shi. Ku ce amin.

Le préfet : Avant de passer à l'intronisation je vous présente mes condolénces pour le décés de l'ancien chef, que Dieu aie pitié de son âme. Dites amen.

Jama'a gaba ɗaya: Amin!

Le public : Amen !

Purepe: An yi maku sabon sarki, akwai abu guda wanda ba ma so. Shi ne tashin hankali. Tashin hankalin talaka, shi ne tashin hankalin parti da gwamnati. To ku kiyaye tashin hankali, idan an kare wanga harakoki. E! *(Purepe ya ɗan tsaya ya yi ɗan tari kafin ya cigaba da cewa)* ina maina….. ?

Le préfet : On vous a choisi un nouveau chef, il y a une chose que nous detestons. C'est le conflit. Si le citoyen n'est pas en paix c'est le gouvernement et le parti qui ne le sont pas. Il faut éviter le conflit après l'intronisation. EH ! *(Le préfret prend une petite pause, tousse un peu avant de continuer)* qui est maina…?

*Mainawa gaba ɗaya suka zaburo suka fito hili suka jera.*

*Tous les princes se précipitent pour répondre et se mettent en rang.*

Maroƙi (*Yana yin kirari) :* Mai rabo ya samu mara rabo ko sai haƙuri. Gaskiya ne! Gaskiya ne!

Le griot *(Faisant les éloges)* : Le chanceux est déjà choisi et que le malheureux soit patient. C'est juste ! C'est la vérité !

Purepe: Wace ce (*Mainawa gaba ɗaya suka zaburo suka fito hili)* maina Salifi?

Le préfet : Qui est (*Tous les princes se précipitent)* maina Salifi ?

Maroƙi: Maina Salihi? Maina Salihi ɗan Baƙoshi.

Le griot : Maina Salifi ? Maina Salifi le fils de « Bakoshi.»

*Maina Salihi ya shigo fili, ya zamna saman tabarma aka sanya mashi babba riga, aka naɗa mashi rawani sannan aka ba shi sanda da takobi ya buga tambari. Aka cigaba da kiɗe-kiɗe da bushe-bushe. Bayan an ƙare naɗi sarki ya tashi ya hawo kujerar sarauta. Maroƙin sarki yana ta yi masa kirari.*

*Intronisation et animation. Après avoir été intronisé, le nouveau roi frappe le tambour royal et s'assoie sur le trône. Le griot du roi lui fait des éloges.*

Maroƙi: A saurara! A saurara dai! Mai nasarawa za ya yi magana. Amin! Amin! Magajin maina Shaho, da kyau insha Allahu! Godiya Allah ta yi.

Le griot : Ecoutez ! Pardon écoutez ! Le chef de Nassaraoua va parler. Amen ! Amen ! Le frère de Chafo, c'est bien, comme Dieu le veut. Merci Dieu…

*Sarki ya tashi ya buga tambari fadawa suka rurufe shi da rigunansu.*

*Le nouveau roise lève pour frapper le tambour royal et les notables le cachent avec leurs boubous.*

Maroƙi: A saurara sarki Salihi za shi yi magana da kansa. Damo sarkin haƙuri, damo sarkin haƙuri.

Le griot : Ecoutez le roi Salifi va prendre la parole. Gueule tapée roi de la patience, Gueule tapée roi de la patience.

Sabon sarki: Bisimillahi Rahamani Rahim. Jama'a mutanen Nasarawa, maza da mata, yara da mayan duka salama alaikum.

Le nouveau roi : Au nom de Dieu le Clément le Miséricordieux. Population de Nassaraoua, hommes et femmes, grands et petits que la paix soit avec vous.

Maroƙi: Amin mai nasarawa!

Le griot : Amen roi de Nassaraoua !

Sabon sarki: Yau, na gode ma Allah, na gode ma ma'aikin Allah (SAW), na gode ma haihuwa uwaye da kakannu, tunda yau na gaji gidanmu.

Le nouveau roi : Aujourd'hui je remercie Dieu, je remercie son Prophète (PSL), je remercie mes parents et mes grands parents, puisque aujourd'hui je viens de les hériter.

*Bugun ganga da taɓi*

*Animation*

Sabon sarki: Saboda haka, du jama'a mutanen Nasarawa, nike kai muku godiya, nike ƙara gaishe ku, tunda kuma kun gwada mani so, kun gwada mani kun yarda da ni, tunda kun so in zama sarkinku in zama shugabanku.

Le nouveau roi : Pour ça, toute la population de Nassaraoua, je vous remercie, je vous salue encore, puisque vous m'avez montré votre amour, vous avez eu confience en moi, vous avez voulu que je sois votre roi que je devienne votre chef.

*Bugun ganga da taɓi*

*Animation*

Maroƙi: Godiya Allah ta yi.

Le griot : On remerci le bon Dieu.

Sabon sarki: Saboda wannan gaban jama'a duka, ina kai godiyata ga manyanmu, manyan partinmu, manyan gwamnatinmu, ubangiji Allah shi yi masu albarka.

Le nouveau roi : C'est pourquoi devant tout le peuple, je salue nos supérieurs, les responsables de notre parti, les chefs du gouvernement que Dieu les bénisse.

Jama'a: Amin mai Nasarawa! Hutawa toron giwa. Habiya sa toron giwa.

La population : Amen roi de Nassaraoua ! Répose-toi grand chef. Compliments.

Fadawa: Amin!

Les notables : Amen !

Sabon Sarki *(Aka buga tambari)* : To kuma ina so gaban manyan nan namu, in jawo hankalin ƴan uwana mainawa wa'anda muka nemi saurata tare.

Le nouveau roi *(On frappe le tambour)* : Et puis je veux devant nos supérieurs attirer l'attention de mes frères avec qui on a compéti ensemble.

Maroƙi: Lumfasawa toron giwa!

Le griot : Mes respects grand chef !

Sabon sarki: Abun da nike so in gaya maku gaban manya ku gane, gidan nan, namu ne na mu duka. Ko cikin dare ko da rana, in wani abu ya same ku ya kamata ku gan ni. Ni ma in wani abu ya samu zan neme ku in neme ku shawara. Saboda kirkin gidan nan, kirkin namu ne na mu duka gaba ɗaya. Assalama alaikum.

Nouveau roi : Ce que je veux vous faire comprendre devant nos chefs, le palais nous appartient tous. Quelqu'en soit le moment si vous avez envie de quelque chose il faut venir me trouver. Moi même en cas de besoin je chercherai conseil auprès de vous. L'honneur de cette maison est pour nous tous. Que la paix soit avec vous !

*Aka jima ana ta yin kiɗa da busa maroƙi yana ta yi wa sabon sarki kirari.*

*Animation et éloges du Le griot du roi.*

Biya maradi**:** Depite ina da magana.

Biya maradi : Monsieur le député je veux parler.

Depite: A'a! Biya maradi ka zamna! In an tashi ka same ni a can gidan parti. Zamna! Kai Allah raba mu!

Le député : Non! Biya maradi assieds toi ! A la fin de la cérémonie tu me trouves au bureau politique. Assois-toi ! Que Dieu nous en garde !

*Aka ci gaba da annashuwa*

*Animation*

Maroƙi: A saurara! Depute nasonal, depute nasonal za ya magana, a saurara ƙusoshin duniya, sarakunan duniya kuke zuwa duniya kuna ganin abin da duniya take ciki.

Le griot : Votre attention ! Monsieur le député national, le député national va parler, écoutez ceux qui ont les nouvelles du monde, les chefs mondials c'est vous qui faites le tour du monde et vous observez ce qui se passe.

Depute: Jama'a maza da mata mutanen Nasarawa salama alaikum.

Le député : Population de Nassaraoua, hommes et femmes, que la paix soit avec vous.

Maroƙi: Amin depite nasanal!

Le griot : Amen monsieur le député national !

Depite: Da ba ni da niyya yin magana. Amma sabada waɗanda suka yi magana yanzu, sun faɗi waɗansu kalmomi, waɗanda nake so in ƙara bayyana maku su.

Le député : Je n'ai pas l'intention d'intervenir. Mais à cause de ceux qui viennent de prendre la parole avant moi, ils ont parlé de certaines choses que je vais vous expliquez.

Maroƙi: Amin!

Le griot : Amen !

Depite: A cikin zancen mai girma "Préfet", shugaban tahiyarmu, ya ce mu yi mashi gafara sabada ba ya jin hausa. To jama'a in kun lura ha kullun, a du lokacin da muka tara jama'a, jawabinmu na hwarko shi ne, mu duka ƴan Nijar, bugaje, abzunawa, barebari, hulani, zabarmawa da mu hausawa, mu duka ƴan ƙasa ɗaya ne, ƴan gari ɗaya ne, ƴan gida ɗaya ne, ƴan ɗaki ɗaya ne.

Le député : Dans le discours du préfet, le chef de notre déléguation, il a demandé pardon parcequ'il ne parle pas bien le haoussa. Oh, peuple si vous pretez attention à chaque fois que nous nous reunissons, notre premier discours est que nous sommes tous des Nigeriens, les touaregs, les abzounawas, les kanouris, les peuls, les zarmas et nous les haoussas, nous

sommes issus d'une même nation, d'une même ville, d'une même maison et d'une même famille.

*Aka taɓa, makiɗa suka buga ganga. Depite ya ci gaba da jawabinsa*

*Animation. Le député continue son discours*

Depite: Bayan haka nan, « préfet » ya ce parti kinmu da gwamnati, ba sa son tashin hankali, wannan gaskiya ne. Sabada kun san mu depite, ana aikamu mayan ƙasashe na Apirika ko na turawa muna wakilta ƙasamu bisa kan shawarwari na al'amuran duniya, muna ganin yadda ake ɗauka mu da daraja sabada zama lahiya da ƙasamu take da shi. Wanda du ya ce zai ɓata mana zaman lahiyan nan ya tabbata parti kinmu da gwamnati ba za su yahe mishi ba.

Le député : Ensuite, Monsieur le Préfet a dis que notre parti et le gouvernement m'aiment pas de conflit, ça c'est la vérité. Puisque vous savez que nous les députés on nous envoie dans les grands pays Africains ou Européens pour répresenter notre pays sur les situations du monde, nous voyons comment on nous considère parceque il y a la paix dans notre pays. Tout celui qui entrave cette paix notre pays et notre parti ne vont pas le lui pardonner.

*Aka taɓa makiɗa suka buga ganga*

*Animation*

Maroƙi: Amin depite nasanal!

Le griot : Amen monsieur le député national !

Depite: Bayan haka nan, magatakarda ya yi butun taimako, lalle kan taimako mun bada shi. Kuma jama'a nasarawa da mutunen ƙasarmu ta Nijar gaba ɗaya sai in ce albishirinku. Dan kun san, shekaru dayawa ruwan sama ya yi ƙaranci, ba a nan ƙasamu ta Nijar kawai ba, hamma a yawancin ƙasashen duniya. Akwai inda tsananin hwari ya sa mutane suna mutuwa, bisashe suna mutuwa, mutane suna galabaita sabada ƙishirwa. Akan haka nan parti kinmu da gwamnatin mun je wurin mayan ƙasashe na turawa waɗanda suka cigaba mun samo wasu mayan jirage, a cikin wannan jirage akwai kayayyakin hikima suna harbin hadarin nan sai ruwa ya kece.

Le député : Ensuite, le sécretaire général a parlé de l'aide, bien sûr nous avons donné de l'aide. Ceci dit, population de Nassaraoua et tout le peuple Nigerien j'ai une bonne nouvelle pour vous. Vous savez pendant des années la saison pluvieuse a été mauvaise pas seulement dans notre pays mais aussi dans d'autres pays du monde. Il y a là où la

sécheresse à fait que les gens meurent, les animaux déciment, les gens sont affablis à cause de la soif. Pour ça nôtre parti et le gouvernement nous sommes allés dans les grands pays Européens qui sont plus developpés pour avoir de grands avions qui sont équipés de matériels qui permettent de tirer les nuages pour que la pluie tombe.

*Aka taɓa makiɗa suka buga ganga*

*Animation*

Depite: Mun tabbata cikin sarautar Allah in ni'ima ta samu albarka ta shiga. Jama'a Nasarawa, kun daɗe kuna jiran mu, ina san in yi amfani da muƙamina na depite nasanal, in miƙa gaisuwarmu zuwa ga ƴan uwanmu wanda muka gayato suka zo bikin naɗin sarauta tun daga Nijeriya.  Wannan yana kwatanta mana tsohon zumuncin nan wanda muka gada tun lokacin kakannin kakanninmu. Dan, in muka diba tarihin Nijar da Najeriya abu ɗaya ne. In kuma muka aje tarihin, muka ɗauki yau, yanzu, gobe, jibi ko gata, daga nan har Ibadan in kun diba mutanen Difa da na Maiduguri ƙabilu guda ne, mutanen Damagaram da na Daura da na Kano stat ƙabilu guda ne, mutanen Maraɗi da na birnin Katsina ƙabilu guda ne, mutanen Tawa da na  Illela da na Sakwato ƙabilu guda ne, mutanen Doso, da na Kamba da na Arungungu ƙabilu guda ne. Dan hakanan ƴan Nijeriya in suka zo a nan ƙasamu ta Nijar, ƙasasu ce, garinsu ne, gidansu ne, haka mu kuma in muka je Najeria ƙasamu ce, garinmu ne, gidanmu ne. Jama'a sai mu ƙarasa da fatan Allah ya taimaki shugabanin ƙasashenmu biyu, Allah ya ɗaga tutocin ƙasashenmu biyu, Allah ya taimaki al'umma kasashenmu biyu baki ɗaya. Salama alaikun.

Le député : Nous sommes certains qu'avec l'aide de Dieu si la pluie tombe le bonheur est trouvé. Population de Nassaraoua je sais bien que vous avez duré à nous attendre, je profite de mon honneur de député national pour souhaiter la bienvenue  à nos invités venus du Nigeria pour l'intronisation. Cela montre cette vieille solidarité que nous avons héritée de nos ancêtres. De part l'histoire, le Niger  et le Nigeria c'est un et un seul pays. A part l'histoire si nous prenons aujourd'hui, maintenant, demain, après demain ou  le lendemain d'ici jusqu'à Ibadan si vous regardez la population de Diffa et celle de Maidougouri sont une même ethnie; celle de Damagarame, Daoura et de Kano sont une même ethnie, la population de Maradi et Birnin Katsina  sont une même ethnie, la population de Tahaoua, Ilélla et de Sokoto sont une même ethnie; la population de Dosso, Kamba et celle de Aragoungoun sont une même ethnie. C'est pourquoi les gens du Nigeria s'ils viennent ici au

Niger, c’est leur pays, leur maison, leur ville, de même nous les Nigeriens si nous partons au Nigeria c’est notre pays, c’est notre maison. Chère population, nous terminons en priant Dieu de venir en aide aux dirigeants de nos deux pays, qu’Allah porte nos flambaux haut, qu’Allah aide tous les peuples de nos deux pays. Que la paix soit avec vous !
*An cigaba da harakokin bikin wakan sarauta ana ta ƴin bushe-bushen algaita da kaɗe-kaɗen ganga.*
*Animation*

**TABLEAU VII**

Biya maradi (*Shi kaɗai a zamne) :* Ni gidan nan, da dukiyata, aka zo aka mumu ba zata? Tun daga manyanmu muna gani aka naɗa shi mu aka bar mu a haka. Ƴan uwana wanda aka san mu da su kullun, yanzu ban san abin da za a yi ba. Ko in kiraye su in nemi gahwara? Koda yake nine babba in kiraye su shawara in ya so gaba ɗaya mu shiga kishin gidanmu mu hwaɗa shi mu gani abin da zai abkuwa. Haka za a yi. Laɓaɓa! Laɓaɓa!

Biya maradi *(Assis seul dans sa cour)* : Moi dans cette maison on vient me surprendre, avec toute ma richesse ? Nos gouvernants sont venus l’intronisé et nous ont laissé sans rien. Maintenant je ne sais pas quoi faire, mes frères et moi avec qui je suis tous les jours. Est-ce que je dois les appeller pour leur demander pardon ? Puisque je suis l’ainé, je vais les chercher, nous allons nous consulter et ensemble nous allons conquérir notre maison, nous l’attaquons pour voir ce qui va se passer. On va faire comme ça. Lababa ! Lababa !

Laɓaɓa: Iyu!

Lababa : Oui !

Biya maradi: Tashi ka je ka kira mini maina Mushe da maina Ɓaidu.

Biya maradi : Vas-y m’appeller maina Mouché et maina Ɓaidu.

Laɓaɓa: Tau!

Lababa : D’accord !

Biya maradi: Ka ce ina kiran su. Maza!

Biya maradi : Dis leur que je les appelle. Fais vite !

Laɓaba: Tau !

Lababa : D’accord !

Biya maradi: Tashi!

Biya maradi : Lève-toi !

*Laɓaɓa ya tashi ya tafi kiran sauran mainawa.*

*Lababa se lève pour aller appeler les autres princes.*

Biya maradi: Wannan shi ne sha'ani? Kai duniya, ikon Allah!

Biya maradi : Ça c'est  quelle affaire ? Vraiment ce monde, mon Dieu !

Laɓaba: Biya maradi ga su nan zoke.

Lababa : Biya maradi ils arrivent.

Biya maradi: Tau!

Biya maradi : D'accord !

Maina Mushe da maina Ɓaidu: Salamu alaikun!

Maina Mouché et maina Baidou : Que la paix soit avec vous !

Biya maradi: Amin alaika wassalam!

Biya maradi : Amen de même que vous !

Maina Mushe da maina Ɓaidu: Yaya!

Maina Mouché et maina Baidou : Grand frère !

Biya maradi: Iyi!

Biya maradi : Oui ?

Maina Mushe: Yaya!

Maina Mouché : Grand frère !

Biya maradi: Kun zo? Muna lahiya?

Biya maradi : Vous êtes là ? Comment vous allez ?

Maina Mushe da maina Ɓaidu: Lahiya lau! Lahiya lau hwa!

Maina Mouché et maina Baidou : Très bien ! Très bien !

Biya maradi: Lahiya! Sannu-sannunku. Ina wahaloli?

Biya maradi : Bien ! Bonne arrivée ! Et la fatigue ?

Maina Mushe: Wahala to ai shi kenan ba komi.

Maina Mouché : La fatigue  ça ne fait rien.

Biya maradi: Kai wannan sha'anin?

Biya maradi : Et cette situation ?

Maina Mushe: Wannan sha'ani? Kana ga dai yadda muka zama?

Maina Mouché : Cette situation ? Tu as vu comment nous sommes devenus ?

Maina Ɓaidou: Abun na mu duka ne ai.

Maina Baidou : Cette affaire nous conserne tous.

Biya maradi: Um! Ƙwarai kwa. Wai nine wai sarki wannan wai hal dige wai ɗiyata aka sa lalle na ce aje a gaya wa sarkin makaɗa ya zo ya yi kiɗin armen da za a yi, wai sai cewa ya yi wai makaɗinshi shi ba ya zuwa ya kaɗa wa ɗiyal maina kiɗa. Yanzu dole sai makaɗan hwarauta na kirawo su za su zo su kaɗa.

Biya maradi : Hum ! Très bien. C'est à moi que ce roi va faire cela, il y a ma fille qui se marie, j'ai envoyé me chercher le chef des griots pourqu'il vienne animer la cérémonie du mariage mais il me dit que son griot ne vient pas jouer pour la fille de maina. Maintenant je suis obligé de chercher le griot des chasseurs pour ça.

Maina Ɓaidu: Shi sarkin shi ya hana su zo?

Maina Baidou : C'est le roi même qui les a empeché ?

Biya maradi: I! I mana.

Biya maradi : Oui ! Oui bien sûr.

Maina Ɓaidu: Ƴan hwarauta sun zo?

Maina Baidou : Les griots des chasseurs sont venus ?

Biya maradi: A'a, sun zo, su na sa.

Biya maradi : Oui ils sont venus, c'est eux que j'ai chargé.

*Juju ya zo wajen su maina Shaho.*

*Joujou va vers les maina Chafo.*

Biya maradi: Koma ka zamna dan Allah, kana gani mu masu hankali ma ba mu samu sarauta ba, balle kai mahaukaci ka zo ka ce, ka zamna tunda maina ne kai ma a yi shawara da kai.

Biya maradi : Vas t'assoir pour l'amour de Dieu, nous même qui sommes des gens normaux n'ont pas été élus à plus forte raison toi qui est débile. Vas t'assoir puisque tu es aussi un prince on va faire la réunion avec toi.

Maina Mushe: Yanzu makaɗan hana su ya yi ko?

Maina Mouché : Maintenant il a refusé à ses griots de venir ?

Biya maradi: Hana su ya yi.

Biya maradi : Il les a empêchés.

Maina Mushe: Ba an kirawo waɗancan makaɗan hwarauta ba?

Maina Mouché : Tu as appellé les griots des chasseurs non ?

Biya maradi: Na sa an kira su.

Biya maradi : Je les ai fais appellé.

Maina Mushe: To shike nan.

Maina Mouché : Donc c'est fini.

Biya maradi: Na ce, ni bari tsakani na da shi sai dai kange.

Biya maradi : J'ai dis qu'il n'ya plus rien entre nous, c'est fini lui et moi.

Maina Mushe: A, to! Ai ni wallai abun sarauta nan mamakin da ya bani ba kaɗan ba ne.

Maina Mouché : Ah oui ! Je le jure, l'intronisation là m'a beaucoup surprise.

Biya maradi: Um!

Biya maradi : Oui !

Maina Mushe: Dan ida ka lura yaya …

Maina Mouché : Si tu as remarqué grand frère…

Biya maradi: Um!

Biya maradi : Oui !

Maina Mushe: Kan mai girma Préfet ya zo inda ka lura ka ga ina zuwa ina komowa?

Maina Mouché : Avant l'arrivée du Préfet as-tu remarqué que je faisais des va- et-viens ?

Biya maradi: I, na gani kana kai kana kawowa.

Biya maradi : Oui, je te vois aller et revenir.

Maina Mushe: Dan ni na tabbta ni za a wa.

Maina Mouché : Parceque j'étais sûr que je serai élu.

Biya maradi: Ina! Ina !

Biya maradi : Loin de Là ! Loin de Là !

Maina Mushe: Ina, sai na ji an kiri wani ba ni ba.

Maina Mouché : A ma grande surprise j'entends appeller le nom de quelqu'un qui n'est pas moi.

Biya maradi: Ina! Ina!

Biya maradi : Loin de Là ! Loin de Là !

Maina Ɓaidu : Ya wuce ni ? Ya wuce ni ? Ni tsohona da za ya mutuwa ya kirayi du hwadawan ya ce ya bada ni amana.

Maina Baidou : Pas plus que moi ! Pas plus que moi ! Moi, qui mon père avant de mourir a appellé tous les notables et m'a confié à eux.

Biya maradi: Kai? Yo, yo, kai hwa ina. Kai hwa ina. Wannan sha'ani an yi dai.

Biya maradi : Toi ? Et, et toi non. Et toi non. Cette affaire c'est fait.

Maina Mushe: Ban san ko kun ji lokacin da yake buga tambarin ba? Ai bai buga sha biyun ba.

Maina Mouché : Avez-vous compté au moment où il frappe le tambour ? Il n'a pas frappé douze fois.

MainaƁaidu: Ni ma na ƙilga sha ɗaya ya yi.

Maina Baidou : Moi même j'ai compté onze fois.

Biya maradi: Sha ɗaya?

Biya maradi : Onze fois *?*

Maina Mushe: Ni ma sha ɗaya na ƙilga.

Maina mouché : Moi aussi c'est onze fois que j'ai compté.

Biya maradi: Sha ɗaya? Awo bai ya shekara, in Allah ya yarda ba ya shekara.

Biya maradi : Onze ? Il ne va pas durer un an, avec la volonté de Dieu il ne fera pas un an au trône.

Mainawa: Sha ɗaya; sha ɗaya ne.

Les princes : Onze, c'est onze fois.

Biya maradi: Tunda dai tambari mu na galgajiya na gidanmu sha biyu ake bugawa.

Biya maradi : Puisque notre tambour traditionnel, celui de notre famille on le tape douze fois.

Maina Mushe: Inhum!

Maina Mouché : Oui !

Biya maradi: Tunda ya buga sha ɗaya to ba ya shekara.

Biya maradi : Puisqu'il a tapé onze fois il ne fera pas un an au trône.

Maina Mushe da maina Ɓaidu: Haka nan ne.

Maina Mouché et Maina Baidou : C'est comme ça.

Biya maradi: E, ba ya shekara.

Biya maradi : Oui, il ne fera pas un an.

Maina Ɓaidu: Ni ma sha ɗayan na gani.

Maina Baidou : Moi même c'est onze que j'ai vu.

Maina Mushe: Makaɗan sun zo ko ba su zo ba?

Maina Mouché : Les griots sont là ou pas ?

Biya maradi: Sun zo su.

Biaya maradi : Ils sont arrivés.

Maina Mushe: To mu yi abun da ke gabanmu.

Maina Mouché : Donc faisons ce que nous devons faire.

Maina Ɓaidu: Laɓaɓa ake turawa ya kira su. In kun gan su to shi kenan. Ko ba haka ba?

Maina Baidou : On envoie Lababa les appeller. Il suffit que vous les voyiez. Ou bien ce n'est pas ça ?

Maina Mushe: E!

Maina Mouché : Oui !

Biya maradi: In kun gan su in ya so shi kenan.

Biya maradi : Il suffit que vous les voyiez et c'est fini.

Maina Mushe: Biki ko yi za a yi.

Maina Mouché : Le mariage aura bien lieu.

Biya maradi: In Allah ya yarda!

Biya maradi : Si Dieu le veut bien !

Maina Mushe: Biki ko yi za a yi.

Maina Mouché : Le mariage aura bien lieu.

Biya maradi: Don ya tabbata, abu da mu kuma. Kan ga *(ya hiddo wuƙa ya gwada wa sauran abokansa)* mu a shirye muke.

Biya maradi: Pour qu'il confirme, que nous faisons parti de la chose. Vous voyez *(Fait sortir un couteau et le montre à ses amis)* nous sommes prêts.

Maina Mushe: Gaskiya ne, i, gaskiya ne.

Maina Mouché : C'est la vérité, oui, c'est la vérité.

Biya maradi: Tun a yi abun sarautal wannan ba na rabuwa da babarbara. A'a! Yo ni!

Biya maradi : Dépuis l'intronisation je me promène toujours avec un couteau. Non ! Moi !

Maina Mushe: Makaɗanshi shi aje abinshi, shi aje makaɗanshi.

Maina Mouché : Qu'il garde ses griots, qu'il les garde.

*Makaɗan farauta suka shigo.*

*Les griots arrivent.*

Makaɗan farauta: Allah shi Biya maradi!

Chasseurs : Votre Majesté !

Mainawa: Yauwa sannu-sannunku!

Les princes : Soyez le bien venu !

*Makaɗan sun fara kiɗi Biya maradi ya tashi yana zanzana yana karya takobi da wuƙa.*

*Les griots animent, Biya maradi en transe casse le couteau en petits morceaux.*

Mainawa: Kai, assha, assha! Haba yaya? Haba yaya?

Les princes : Mon Dieu ! Ce n'est pas possible ! Pardon grand frère ? Pardon grand frère ?

Maina Mushe: Ai ni wannan abu ya bani mamaki.

Maina Mouché : Vraiment cela ma surpris.

Ƴan aiken sarki: Salama alaikun!

Envoyés du roi : Que la paix soit avec vous !

Maina Mushe: Laɓaɓa a kai makaɗan ga gida, a dama masu hura, a dama masu hura. E, a tai gida.

Maina Mouché : Lababa, il faut amener ces griot à la maison, donner leur du foura. Oui, allez-y à la maison.

*Maina Mushe da maina Ɓaidou suka tashi suka kame biya maradi kuma suka amshe wuƙar ga hannunsa.*

*Maina Mouché et maina Baidou arrachent le couteau des mains de Biya maradi.*

Maina Ɓaidu: Haba yaya!

Maina Baidou : Pardon grand frère ?

Ƴan aiken sarki: Salama alaikun!

Envoyés du roi : Que la paix soit avec vous !

Maina Mushe: Biki sai da marece. E, ku tai gida biki sai da marece.

Maina Mouché : Pour le mariage il faut le soir. Oui, vas-y à la maison, le mariage il faut le soir.

Ƴan aiken sarki: Biya maradi! Biya maradi!

Les envoyés du roi : Biya maradi ! Biya maradi !

Biya maradi: Wai mine ne? Lahiya?

Biya maradi : Qu'est ce qu'il y a ?  C'est quoi ?

Ƴan aiken sarki: E, sarki ya turo mu, ya ce…

Les envoyés du roi : C'est le roi qui nous a envoyé, il a dit…

Maina Mushe: Kana ji?  Zancen yarinya da aka butun aurenta.

Maina Mouché : Tu m'enttends ? Je te parle de la fille qui va se marier.

Ɗan aike: Ya ce…

Un envoyé du roi : il a dit…

Maina Mushe: A, kai don Allah ka bari, akwai harakokin da a gabanmu.

Maina Mouché : E, toi laisse nous, nous avons d'autres choses devant nous.

Ɗan aike: To, ƙaƙa ya bari? Ana zancen sarki……

Un envoyé du roi : Comment va-t-il se taire ? On parle du roi…

Biya maradi: Kanga ni, rihe mini bakinka!

Biya maradi : Tu vois, fermes-moi ta bouche !

Ɗan aike: An ce sarki ya aiko.

Un envoyé du roi : On a dit que c'est le roi qui a envoyé…

Biya maradi: Jeka ka ce mashi mun ƙi ban ma zuwa. Ƴan gidansa ne mu ko bashi yake bin mu? Jeka ce ban ma zuwa.

Biya maradi : Retournes lui dire que nous n'irons pas. Sommes-nous ses sujets ou bien nous avons une dette en vers lui ? Vas lui dire que nous n'irons pas.

Maina Mushe: Sarkin dogarai dakata, dakata. Biya maradi!

Maina Mouché : Attends chef des notables, attends. Biya maradi !

Ƴan aiken sarki: Biya maradi dakata.

Les envoyés du roi : Un instant Biya maradi.

Biya maradi: Da wani rigaka iri-iri kama karen Allah.  Ka zo kakaka dame mu a cikin gidana. In sarki ne ya aikoka ƙwaci, ko sarki ya aiko ka a tilas ka zo.

Biya maradi : Avec ton boubou qui resemble à un arc-en-ciel. Tu viens chez moi nous déranger. Viens nous obliger puisque c'est le roi qui t'a envoyé, même si c'est le roi qui t'a envoyé tu es obligé de venir.

Ɗan aike: Biya maradi, in ka je wurin kiran wannan, sai ka ban tukwici, daga kai ha ƴan uwan naka wannan.

Un envoyé du roi : Biya maradi, si tu réponds à l'appel du roi tu vas me donner un cadeau, et même tes frères.

Mainawa: To ku je! Ku ce mai muna zuwa. Ku tahi ba komi. Ku je!

Les princes : Allez-y ! Dites lui que nous arrivons. Ça ne fait rien. Allez-y !

Maina Mushe: Ka ga da su aka game kai aka yi ƙumbiya-ƙumbiyan da akai wa sarkin nan sarauta.

Maina Mouché : Tel que tu les vois c'est avec leur complicité que ce roi a été élu.

Biya maradi: E! Manyan munahukai na Nasarawa.

Biya maradi : Oui ! Les grands hypocrites de Nassaraoua.

Maina Mushe: Wai ku je sarki yana kiran ku. Mi yaka nema gare mu?

Maina Mouché : Allez-y le roi a besoin de vous. Qu'est ce qu'il veut de nous ?

Maina Ɓaidu: Wai ha tukwici za a ba shi.

Maina Baidou : Et puis on va même lui donner un cadeau.

Biya maradi: To ban na zuwa kiran nashi.

Biya maradi : Bon je ne réponds pas à son appel.

MainaMushe: Ba mu zuwa. Yanzu mu yi abun da a gabanmu.

Maina mouché : Nous n'irons pas. Maintenant faisons ce que nous devons faire.

Biya maradi: I!

Biya maradi : Oui !

Maina Mushe: Auren yarinya ko yi za a yi.

Maina Mouché : Le mariage de cette fille aura bien lieu.

Biya maradi: An sa rana.

Biya maradi : On a fixé la date.

Maina Ɓaidu: Ba shi kenan ba? Yaushe ne ake bikin?

Maina Baidou : c'est fini non ? Quand auront lieu les cérémonies ?

Maina Mushe: Biki gobe ne.

Maina Mouché : Les cérémonies sont pour demain.

Biya maradi: I, gobe ne.

Biya maradi : Oui, c'est demain.

Maina Mushe: Amma, yaya ko ba gaskiya ba?

Maina Mouché : Mais grand frère, ou bien ce n'est pas ça ?

Biya maradi: Um!

Biya maradi : Oui !

Maina mushe: Ya kamata mu tai mu ji kiran da ya kai muna. Bai dai kashe mu?

Maina Mouché : Il est convenable que nous répondions à son appel.Il ne va pas nous tuer non?

Biya maradi: Um!

Biya maradi : Oui !

Maina Mushe: Ji yaya.

Maina Mouché : Ecoute grand frère.

Biya maradi: Kun shirya tukun?

Biya maradi : Etes-vous prêt ?

Mainawa: A shirya kowa yake.

Les princes : Nous sommes tous prêts.

Maina Mushe: Iyaka ya gan mu ko?

Maina Mouché : Qu'il nous voit tout simplement non ?

Shaho: I!

Chafo : Oui !

Mushe: To mutai mu ji ko mine ne.

Mouché : Allons-y voir de quoi il s'agit.

Biya maradi: Kuma ni in na je ko gaida shi ban na yi.

Biya maradi : Et puis moi quand je vais, je ne vais même pas le saluer.

Biya Baidou: Wane shi. E!

Maina Baidou : Qui est-il ? Oui !

Maina Mushe: To mu dai mu tai.

Maina Mouché : Donc allons-y.

Maina Ɓaidu: In ya so ya kashe mu.

Maina Baidou : S'il veut qu'il nous tue.

Biya maradi: Wane shi?

Biya maradi : Qui est-il ?

Maina Mushe: Ku tai mu tai !

Maina Mouché : Allons-y !

Biya maradi: Ai!

Biya maradi : Oh !

**TABLEAU VIII**

*Mainawa suka tashi zuwa fadar sarki in da suka tarda fadar cike da mutane ana bushe-bushen algaita da kide-kiɗe. Sarki yana zamne tsakar fada.*

*Les princes sont arrivés à la place du chef où ils ont trouvé une grande animation. Le roi assis au milieude ses notables.*

Ƴan aiken sarki: Allah ƙara ma daraja!

Les envoyés du roi : Que Dieu augmente ta grandeur !

Fadawa: Amin, sarkin dogarai. Lafiya sa!

Les notables : Amen, chef des notables. Paix à toi !

Ƴan aiken sarki: Allah baka nasara, mun je.

Les envoyés du roi : Votre Majesté, nous sommes allés.

Sabon sarki: Kun same su?

Le nouveau roi : Vous les avez trouvés ?

Ƴan aiken sarki: Mun same su.

Les envoyés du roi : Nous les avons trouvés.

Sabon sarki: Kun tarda su Mushe da su Ɓaidun duka?

Le nouveau roi : Vous avez trouvé Mouché et Baidou *?*

Ƴan aiken sarki: Duka gaba ɗaya mun tarda su. Suna zauwa. Amma hwa gidan ba dama.

Les envoyé du roi : Nous les avons tous trouvés. Ils arrivent. Mais seulement ça ne va pas chez lui.

Sabon sarki: Um! Da aka yi mi?

Le nouveau roi: Oui ! Qu’est ce qui c’est passé ?

Ƴan aiken sarki: Ana kaɗe-kaɗe, ana karya wuƙa, ana karya takkuba. Wannan kama kai ka je. Allah baka nasara!

Les envoyés du roi : Il y a une forte animation, on casse des couteaux, on casse des sabres. C’est comme si c’est toi-même qui est parti. Votre Majesté !

*Kiɗe-kiɗe*

*Animation*

Maroƙi: Lumfasawa toron giwa, lumfasawa!

Le griot : Calmez-vous  grand roi, Paix à vous !

*Mainawa sun zo fada ɗaya bayan ɗaya suna durƙusawa su gaida sarki.*

*Les princes rentrent un à un et s'agenouillent pour saluer le roi.*

Fadawa: Amin maina Mushe, amin, amin Ɓaidu, amin, amin Laɓaɓa, amin.

Les notables : Amen maina Mouché, amen Baidou, amen Lababa, amen.

Maroƙi: Lumfasawa toron giwa.

Le griot : Calmez-vous grand roi!

*Kiɗe-kiɗe*

*Animation*

Maroƙi: Lumfasawa toron giwa, lafiya sa!

Le griot : Calmez-vous grand roi, paix à vous !

Sabon sarki: Shaho? Shafo?

Le nouveau roi : Chafo ? Chafo ?

Fadawa: Shaho sarki na kiranka, amshi magana.

Les notables : Chafo le roi t'appelle, répond lui.

Shaho: Ba kunne ba yake ji?

Chafo : C'est l'oreille qui entend non ?

Sabon sarki: Ikon Allah! Ni na tura a buɗo ka.

Le nouveau roi : Mon Dieu ! C'est moi qui ai envoyé te chercher.

Shaho: To, ga ni.

Chafo : Ok, je suis là.

Sabon sarki: Da kai da ƙannunmu duka.

Le nouveau roi : Toi et tous nos frères.

Shaho: Hum!

Chafo : Houm !

Sabon sarki: Dan an zo an ce mini a can gidanka ka tara mutane, ana kaɗe-kaɗe, ana karya wuƙaƙe, ana karya takubbai.

Le nouveau roi : On vient de m'informer que tu as réuni des gens chez toi, il y a une forte animation, on casse des couteaux, on casse des sabres.

Shaho: Um!

Chafo : Oui !

Sabon sarki: Na ce a kiro ka in ji abun da ya hwaru.

Le nouveau roi : C'est pour quoi j'ai dis de t'appeller pour que je sache ce qui se passe.

Fadawa: Lumfasawa toron giwa! Ganinmu ganinka. Allah baka nasara!

Les notables : Calmez-vous  mon roi ! C’est comme si c’est toi qui les a vu. Votre Majesté !

Shaho: Abun da ya hwaru, asiri ƙarya ne?

Chafo : Ce qui c’est passé, le pouvoir magique est réel non ?

Sabon sarki: Ikon Allah!

Le nouveau roi : Mon Dieu !

Maroƙi: Lafiya sa, lumfasawa!

Le griot : Paix à vous ! Calmez-vous  mon roi !

Sabon sarki: Yanzu ka iya dibawa Shaho, tun ran in hawo kujera gidan nan, gaban manyan, na ce maku da ni da ku duka ɗaya ne.

Le nouveau roi : Maitenant regarde Chafo, dépuis le jour de mon intronistion devant nos chefs j’ai dis que nous sommes tous ensemble.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C’est la vérité !

Sabon sarki: Mu ƴan ciki ɗaya ne.

Le nouveau roi : Nous sommes de la même famille.

Fadawa: Insha Allahu!

Les notables : Bien sûr !

Sabon sarki: Na ce maku gidan nan namu ne.

Le nouveau roi : Je vous ai dis que cette maison est la nôtre.

Fadawa: Haka ne!

Les notables : C’est ça !

Shaho: Naka ɗai!

Chafo : C’est ta maison

Sabon sarki: Ikon Allah!

Le nouveau roi : Mon Dieu !

Fadawa: Lumfasawa toron giwa!

Les notables : Calmez-vous  grand roi !

Sabon sarki: Diba hwa a gidan nan kai ne babba gare mu.

Le nouveau roi : Il faut voir dans cette maison tu es notre ainé.

Shaho: Inda nine babba hwa a kasa yi min sarauta kai a baka?

Chafo : Si je suis l'ainé pour quoi on ne m'a pas élu ?

Sabon sarki: Ap! Ai sai ka diba sarauta yin Allah ne!

Le nouveau roi : Ah ! Mais c'est Dieu qui donne le pouvoir.

Fadawa: Haka ne!

Les notables : C'est ça !

Sabon sarki: Wanda Allah ya ba sai a dangana a bi shi.

Le nouveau roi : Tout celui que Dieu a choisi on le suit.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon Sarki: Wata ran ƙila ka hawo, wata ran Ɓaidu ya hawo, wata ran Mushe ya hawo.

Le nouveau roi : Peut être un jour tu seras roi, un jour c'est Baidou, un jour c'est Mouché.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Yadda wasu suka hawo suka shiɗa na hawo, wata ran nima sai in shiɗa wani ya hawo.

Le nouveau roi : Comme d'autres roisont regnés avant moi, un jour moi-même je vais laisser ce trône pour d'autres personnes.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Bai kamata ba kai babbanmu ka rinƙa yin haka nan.

Le nouveau roi : Ce n'est pas normal toi qui es notre ainé et c'est toi qui fais certaines choses.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Kuma an gaya mini kai Mushe ban sani ba an zancen in gaskiya ne? Aka ce ana ma Tsahara arme ko?

Le nouveau roi : Je ne sais pas si vrai Mouché ? On vient de me dire que Tsahara va se marier non?

Maina Mushe: I, gaskiya ne. Ranka ya daɗe!

Maina Mouché : Que Dieu vous prète longue vie ! Oui, c'est la vérité.

Sabon sarki: Yau kuma ƙaƙa ɗiya cikina, dan ɗiyaka ko ɗiya Shaho ko ɗiya Ɓaidu ai ɗiyana ne.

Le nouveau roi : Comment se fait il que ma propre fille, puisque ta fille ou celle de Chafo ou de Baidou sont mes filles.

Fadawa: Insha Allahu!

Les notables : Avec la volonté de Dieu !

Sabon sarki: A ce ana masu arme dan an ce na huta daji kan in dawo a ce ni ba za a gaya mani wannan zance ba.

Le nouveau roi : Ces filles se marient parceque je suis sorti avant mon arrivée on réfuse de m'informer.

Fadawa: Assha! Kuskure ne. Assha!

Les notables : Désolés ! C'est une erreur. Désolé !

Shaho: Ai aikawa muka yi sarkin makaɗanka ya zo ya  yi mumu kida, ka ce baya mumu kiɗi. Wai mu sarkin makaɗanka ba sarkin makaɗan mainawa ba ne, na saraki ne aka hana sarkin makaɗan, sai da muka aika makaɗan hwarauta suka zo. Shi ya sa mu kuma muka tuna asirinmu na iyaye da kakanni muka kakkarya takubbai da wuƙa.  Asiri ai ba ƙarya ne ba. Mun karya.

Chafo : Nous avons envoyé pour que ton griot vienne, tu as dis qu'il ne joue pas pour nous. Ton griot n'est pas le griot des princes, c'est le griot des rois on lui a refusé de venir, il a fallu que j'envoie chercher les griots de chasseurs. C'est pour cela que nous nous sommes rappellés du pouvoir de nos grands parents pour casser les sabres et les couteaux. Le pourvoir magique c'est réel. On a cassé.

Fadawa: Assah! Lumfasawa toron giwa!

Les notables : Désolés ! Calmez-vous  grand roi !

Sabon sarki: Ciroma kana da labarin wannan zancen na tambaya sarkin makaɗa?

Le nouveau roi : Tchiroma tu es au courant de la demande du chef de griots ?

Ciroma: A'a!

Tchiroma : Non !

Sabon sarki: To ai ka ga abun da nike gudun ya hwaru ko. Wato mutane an hwara zuwa wajen su Shaho a je akai masu magana a ɗauko a kawo?

Le nouveau roi : Voilà ce que je crainds c'est produit. Donc les gens ont commencé à allez chez les Chafo pour raconter des histoires et revenir chez moi me les colporter ?

Fadawa: Assha! Ƙwarai kuwa. Assha!

Les notables : Désolés ! Bien sûr ! Désolé !

Sabon sarki: Wadda ba ni son kenan. Yaushe ake ƙare bukin kai Mushe?

Le nouveau roi : C'est ce que je ne veux pas. Mouché les cérémonies finiront quand ?

Maina Mushe: Buki gobe za a somawa.

Maina Mouché : Les cérémonies débuteront demain.

Sabon sarki: To yadda nike so du abun da ake yi, du bukin na ɗauke shi akan kaina.

Le nouveau roi : Ce que je veux je prends en charge toutes les dépenses, tout ce qu'on va faire.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Baƙi duka da suka zo da makiɗa duka da suka zo, gobe da sahe du ku kawo su nan.

Le nouveau roi : Tous les invités qui sont venus et les griots qui sont venus, demain matin il faut tous les amener ici.

Fadawa: Lafiyasa!

Les notables : Paix à vous !

Sabon sarki: Ni za ni yin bikin komi da komi wannan ba bukinku ba ne.

Le nouveau roi : C'est moi qui vais organiser tout et ce n'est pas votre affaire.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Ɗiyata ce, kuma a lahira ita za ni dahwawa.

Le nouveau roi : C'est ma fille même dans l'au déla c'est sur elle que je vais m'appuyer.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Ita ce ɗiyata.

Le nouveau roi : C'est elle ma fille.

Maina Mushe: Ya yi kyau, madalla, ya yi kyau.

Maina Mouché : C'est bien, merci, c'est bien.

Sabon sarki: To kuma kiran da na yi maku, da nike cewa gidan nan namu ne namu duka.

Le nouveau roi : La raison pour laquelle je vous ai fait venir en disant que cette maison est la nôtre.

Fadawa: Insha Allahu!

Les notables : Par la grâce de Dieu !

Sabon sarki: Shaho mutane duka nan ha makaɗa sun sani.

Le nouveau roi : Chafo tous les gens qui sont ici même les griots le savent.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Lokacin sarki Mailahiya, akwai abun da aka biɗa gidan nan ba ka samu ba. Wahala ka yi ta. Matuƙa wahala ka yi mu kanmu mun sani.

Le nouveau roi : Au temps du roi Mailafiya tu as voulu avoir quelque chose dans cette maison mais tu n'as pas eu. Tu as beaucoup souffert. Nous savons que tu as très souffert.

Fadawa: Lumfasawa!

Les notables : Calmez-vous  grand roi !

Sabon sarki: Amman ka ga ha Allah ya yi mishi cikawa bai biya maka wannan buƙata ba.

Le nouveau roi : Mais comme Dieu ne l'a pas voulu jusqu'à sa mort il n'a pas pu te nommer.

Fadawa: Lumfasawa!

Les notables : Calmez-vous  grand roi !

Sabon sarki: Saboda wannan na kire ka ni kuma wajen tada ba ni son biye naka, komi ni za ni biya. Kuma in muka.

Le nouveau roi : C'est pour quoi je t'ai appellé et je ne veux même pas un franc de toi, je vais tout payer. Et je vais te le faire.

Fadawa: Lumfasawa!

Les notables : Calmez-vous !

Sabon sarki: Saboda Yakudima da ka tambaya na ƙasa nan, ba ka samu ba.  Ciroma da kai Galadima da ku duka, jama'a da ke nan yau ku shaida, nama Shaho Yakudima ƙasan nan.

Le nouveau roi : Pour le titre de Yakoudima que tu as demandé, que tu n'as pas eu. Tchiroma et toi Galadima et vous tous, les gens qui sont là, soyez temoins aujourd'hui, je nomme Chafo Yakoudima de ce pays.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Du abun da ya aikata kama ni na aikata.

Le nouveau roi: Tout acte qu'il cause c'est comme si c'est moi qui l'ai fait.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

*An wa Shaho naɗin sarautar Yakudima. An sanya masa babba riga, an bashi takobi. Aka cigaba da bushe-bushe da da kiɗe-kiɗe*

*Chafo est nommé Yakoudima. On l'a habillé en grand boubou et on lui a donné un sabre. L'animation a continué.*

Fadawa: Lumfasawa toron giwa! Lafiya sa!

Les notables : Calmez-vous grand roi ! Paix à vous !

Ɗan aiken sarki: Allah baka nasara, Allah baka nasara.

L'envoyé du roi : Votre Majesté, Votre Majesté.

Sabon sarki: Ina Mushe?

Le nouveau roi : Où est Mouché ?

Fadawa: Mushe ana kira.

Les notables : Mouché on t'appelle.

Ɗan aiken sarki: Da ni da Yakudima.

L'envoyé du roi : C'est entre Yakoudima et moi.

Sabon sarki: Yau mi aka yi?

Le nouveau roi : Mais qu'est ce qui se passe ?

Ɗan aiken sarki: Shi ya sani.

L'envoyé du roi : Lui il sait bien.

Sabon sarki: Yakudima akwai wani zance tsakaninku, ku da shi?

Le nouveau roi : Yakoudima, il y a quelque chose entre vous ?

Yakudima: E!

Yakoudima : Oui !

Ɗan aiken sarki: Tukwici, shi ya sani. Rana wanka ba a ɓoyon cibiya.

L'envoyé du roi : Il sait bien, mon cadeau. Proverbe.

Yakudima: Ka samu.

Yakoudima : Tu l'auras.

Ɗan aiken sarki: Ahan!

L'envoyé du roi : Ah bon !

Fadawa: Lafiyasa toron giya!

Les notables : Paix à vous  grand roi !

Sabon sarki: Mushe?

Le nouveau roi : Mouché *?*

Maina Mushe: Ranka ya daɗe!

Maina Mouché : Longue vie à toi !

Sabon sarki: Ka diba a gidan nan Yakudima kai da yake babba, ku rinƙa ba shi magana. Yana tare da mutane wa'anda ke sa shi muguwa hanya.

Le nouveau roi : Yakoudima, toi qui es l'ainé de cette maison, il faut que vous lui donniez conseil. Il a des amis qui le mettent sur le mauvais chemin.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Ka kiyayi kanka da su.

Le nouveau roi : Il faut les éviter.

Fadawa: Lunfasawa!

Les notables : Calmez-vous !

Sabon sarki: E, suna zowa suna dariya a gidanka muggan mutane ne, akan yanzu mun tambaya, da an ce za a tada ka daga nan, muka ce a barka kusa da mu in za ka huta hanya dai ma taro ka.

Le nouveau roi : Ce sont des mauvaises personnes, bien que nous avons demandé maintenant, on a voulu t'affecter d'ici, nous avons demandé à ce qu'on te laisse à côté de nous quand tu vas dérailler nous allons te ramener sur le droit chemin.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Saboda wannan dan abu na galgajiya a ƙasan nan na ga an barshi, an sake shi.

Le nouveau roi: J'ai constaté que dans ce pays on a laissé tout ce qui est tradition.

Fadawa : Gaskiya ne !

Les notables: C'est la vérité!

Sabon sarki: Ni ko ina son in maido shi. Saboda wannan za a yi mishi magajin gari.

Le nouveau roi : Je veux le réhabiliter.  Pour cela il sera nommé maire de la ville.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

*An naɗa Mushe magajin gari. An sanya masa babba riga, an bashi takobi. Aka ci gaba da bushe-bushe da da kiɗe-kiɗe*

*Intronisation de Mouché et animation*

Maroƙi: Lumfasawa toron giwa ! Lafiyasa!

Le griot : Calmez-vous  grand roi ! Paix à vous !

Sabon sarki: Ɓaidu, ina Ɓaidu?

Le nouveau roi : Baidou, où est Baidou ?

Fadawa: Amsa kira, amsa kira Ɓaidu.

Les notables : Répond, répond Baidou.

Ɓaidu: Allah baka nasara!

Baidou : Votre Majesté !

Fadawa: Amin Ɓaidu!

Les notables : Amen Baidou !

Sabon sarki: Abin da za ni gaya maka…

Le nouveau ro: Ce que je vais te dire…

Fadawa: Lumfasawa!

Les notables : Calmez-vous  grand roi !

Sabon sarki: Ka kiyaye da zamani.

Le nouveau roi : Méfie-toi de cette vie.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Ka ga lokacin da ubanka ke sarki duka gaba ɗaya bin shi muka yi.

Le nouveau roi : Quand ton père était roi nous tous nous l'avons suivi.

Fadawa: Wannan gaskiya ne.

Les notables : Ça c'est la vérité.

Sabon sarki: Ba mu saɓa mai ba.  Allah ya jiƙan shi.

Le nouveau roi : Nous ne lui avons jamais désobéis. Que Dieu lui pardonne.

Fadawa: Amin!

Les notables : Amen !

Sabon sarki: Iya yiwuwa wa'annan mutane masu bin bayanka suna kar ka yarda, an yi mine ne, an yi mi, an yi kaza, an yi kara, an yi icce.

Le nouveau roi : Il se peut que ces gens qui sont avec toi, qui te disent de ne pas être d'accord, de faire ceci, de faire cela, on a fait ceci, on a fait cela.

Fadawa: Lumfasawa!

Les notables : Calmez-vous!

Sabon sarki: Ba haka ba ne.

Le nouveau roi : Ce n'est pas ça.

Fadawa: Lumfasawa!

Les notables : Calmez-vous  grand roi !

Sabon sarki: Kai ma an maka Yarima.

Le nouveau roi : Toi aussi tu es nommé Yarima.

*An naɗa Ɓaidu Yarima. An sanya masa babba riga, an bashi takobi. Aka cigaba da bushe-bushe da da kiɗe-kiɗe*

*Intronisation de Baidou et animation*

Juju *(Juju ya zo gaban sarki):* Na ji ka yi wa ƴan uwana sarauta, niko mi na kashe maka ba a yi min ba? Ko so kake in bine ku da ƙasa?

Joujou *(Joujou se présente devant le roi)* : Qu'est ce que je t'ai fais pour nommer mes frères et me laisser. Tu veux que je vous verse du sable ?

Fadawa da mainawa: A'a, a'a!

Les notables et les princes : Non, non !

Sabon sarki: Yauwa, yauwa biya maradi!

Le nouveau roi : Bien, bien biya maradi !

Juju: Yau ni za a wa sarautal?

Joujou : C'est moi qu'on va nommer ?

Yakudima: Kai za a wa.

Yakoudima: C'est toi qui seras nommé.

Biya maradi: Dakata sarkin dogarai!

Biya maradi : Arrête chef des notables !

Sarkin dogarai: Na'am, ranka ya daɗe.

Le chef des notables : Oui, votre Majesté.

Yakudima: Ka kai shi kasuwa du abun da ake ci…

Yakoudima : Vous allez au marché tous ce qui est consommable…

Sarkin dogarai: Insha Allahu!

Le chef des notables : Si Dieu le veut !

Yakudima: Ya ɗauki ɗaya.

Yakoudima : Qu'il prenne un.

Sarkin dogarai: To!

Le chef des notables : D'accord !

Yakudima: An naɗa shi, shi ne sarkin kasuwar.

Yakoudima : On l'a nommé, c'est lui chef du marché.

*Aka ci gaba da bushe-bushe da da kiɗe-kiɗe*

*L'animation continue*

Fadawa: Lumfasawa toron giwa! Lafiyasa!

Les notables : Calmez-vous  grand roi ! Paix à vous !

Sabon sarki: To, jama'a, Alhamdu Lillahi, abun da nike nihi, a cikin yarda Ubangiji, na same shi. Ba wani abu ba nike nihi haɗa kai da ni da ƴan uwana.

Le nouveau roi : Oh,  peuple, Dieu merci, mes voeux sont exhaussés avec la volonté de Dieu, je l'ai eu. Tout ce que je veux c'est l'union entre mes frères et moi.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Ga shi ko yau Allah ya sada hankalinmu.

Le nouveau ro i: Et voilà aujourd'hui Dieu nous a réuni.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Kan ku hwadawa, ko ku makaɗa, ba ni son wanda zai je ko ya tarda Yakudima ko magajin gari, ko Ciroma a zo a ce mini ga shi abin da aka yi a gidanshi koko a ɗauki zancen gidana a je akai masu.

Le nouveau roi : Et vous les notables ou vous les griots, que personne ne vienne me trouver ou allez chez Yakoudima ou chez le maire ou chez Tchiroma rapporter ce qui se passe chez l'un de nous.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C’est la vérité !

Sabon sarki: Du wanda ya kawo mini wanga zance a nan gidan ina mishi wulaƙanci.

Le nouveau roi : Tout celui qui me rapporte des comèrages verra de quel bois je me chauffe.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C’est la vérité !

Shaho: Dama ni ne mai tsegumin ni ma ko na hwasa.

Chafo : Avant même c’étais moi le comère mais je me suis repentit.

Sabon sarki: To shi kenan.

Le nouveau roi : Donc c’est fini.

Fadawa: Lumfasawa!

Les notables : Calmez-vous  grand roi !

Sabon sarki: Kun sani da ake cewa ƙasa a gama kai, gama kai daga gida ya fara tashi.

Le nouveau roi : Comme on le dit il faut qu’on soit unis dans un pays, l’union commence au sein des familles.

Fadawa: Ina!

Les notables : Jamais !

Sabon sarki: In gama kai bai tashi ba daga gida ba har abada a ƙasa ba za a yin shi ba.

Le nouveau roi : S’il n’y a pas la cohésion dans les familles, il n’y aura pas de cohésion dans le pays.

Fadawa: Ina! Wannan ina!

Les notables : Jamais ! Ça jamais !

Sabon sarki: Saboda wannan ku kiyaye da wannan. Abun da za ni gaya maku kenan.

Le nouveau roi : Pour cela il faut faire attention. C’est tout ce que j’ai à vous dire.

Fadawa: Lafiyasa toron giwa!

Les notables : Paix à vous  grand roi !

*Aka ci gaba da bushe-bushe da da kiɗe-kiɗe.*

*L’animation continue.*

Sabon sarki: Yanzu abin da za a yi Yakudima sabada baƙin wa’annan, baka kawo baƙo ka bar shi ha yunwa ta dame shi.

Le nouveau roi : Maintenant ce qu'il y a lieu de faire Yakoudima pour ces invités là, tu ne peux pas inviter quelqu'un et le laisser sans manger.

Ɗan aiken sarki: Allah baka nasara! Masu karye-karyen wuƙa, a nemo mutanen nan.

L'envoyé du roi : Votre Majesté ! Il faut envoyer chercher les gens là qui cassent le couteau.

Sabon sarki: An ce hwa ka tara  mutanen wa'annan masu karye-karyan wuƙa? Ka yi shiru ko baka so ka gwadamumu ?

Le nouveau roi : Il parait que tu as réuni des invincibles chez toi ? Tu ne dis rien ou bien tu ne veux pas nous les montrer.

Yakudima: Ai yanzu mu naka ne duka, ranka ya daɗe.

Yakoudima : Maintenant nous sommes tous à toi, votre Majesté.

Fadawa: Lafiyasa!

Les notables : Paix à vous !

Sabon sarki: To a kawo su in gani, a kawo su in gani.

Le nouveau ro: Amenez-les je veux les voir, amenez-les je veux les voir.

Yakudima: Laɓaɓa ce su zo.

Yakoudima : Lababa dis leur de venir.

Sabon sarki: In sun yi wani shiri ne sai mu tai gaba ɗaya.

Le nouveau roi : S'ils sont prêts nous allons partir ensemble.

Fadawa: Lafiyasa!

Les notables : Paix à vous !

Yakudima: A to ai yanzu du naka ne mu duka.

Yakoudima : Maitenant nous sommes tous à toi.

Sabon sarki: To shi kenan.

Le nouveau roi : Donc c'est fini.

Makaɗan farauta: Allah baka nasara!

Les griots de chasseurs : Votre Majesté !

Fadawa: Amin!

Les notables : Amen !

*Makaɗan farauta suka fara kiɗa da waƙar farauta. Baushi ya shigo cikin fili ya yi kirari yana zanzana da takobi a hannunshi. Zangina ɗan tauri ya shigo yana taka ƴa rawa ya yi kirari. Wani dan tauri ya sake shiga fili yana kirari.*

*Les griots des chasseurs chantent et battent le tam-tam. Bauchi entre et fait son éloge en tremblant avec un couteau à la main. Zanguina l'invincible lui aussi vient en dansant et fait ses éloges*

Fadawa: Lumfasawa toron giwa, lafiyasa!

Les notables Calmez-vous grand roi ! Paix à vous !

Sabon sarki: Yakudima!

Le nouveau roi : Yakoudima !

Yakudima: Na'am, Allah baka nasara!

Yakoudima : Oui, votre Majesté !

Sabon sarki: Lalle shirin naka, ashe shirin ba na wasa ba ne.

Le nouveau roi : Certe ton plan, n'est pas du tout mauvais.

Yakudima: Ai wannan kaɗan ne.

Yakoudima : Mais ça c'est petit.

Sabon sarki: Kaɗan ne wannan?

Le nouveau roi: C'est petit ça ?

Fadawa: Lumfasawa toron giwa, lafiyasa!

Les notables Calmez-vous grand roi, paix à vous !

Sabon sarki: Shi wannan yaron ba irin su sarkin yaƙi Ɗan Cimma ba ne?

Le nouveau roi : Ce garçon ce n'est pas le petit fils du chef de guerre Dan Tchimma ?

Fadawa: Jikanshi ne.

Les notables : C'est son petit fils.

Sabon sarki: Yauwa, da alamu.

Le nouveau roi : Bien sûr, ils se ressemblent.

Yakudima: I, mana!

Yakoudima : Oui, bien sûr !

Sabon sarki: Yau ai ka san da yake muna cikin abu na galgajiya.

Le nouveau roi : Comme nous sommes dans les choses de la tradition.

Yakudima: I, gaskiya ne!

Yakoudima : Oui, c'est la vérité !

Sabon sarki: Wanda aka hwara bari, ya hwara ɓacewa.

Le nouveau roi : Celui qu'on a commencé à délaisser, ça commence à disparaitre.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Ya kamata tunda akwai irin su…

Le nouveau roi : Puisqu'il y a des héritiers…

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: Mu maida sarkin yaƙi a ƙasa nan tamu.

Le nouveau roi : Il faut réhabiliter le chef de guerre dans notre terroir.

Fadawa: Gaskiya ne!

Les notables : C'est la vérité !

Sabon sarki: An naɗa masa sarkin yaƙi.

Le nouveau roi : Il est nommeé chef de guerre.

*Sarkin yaƙi ya shigo fili aka yi mashi naɗi.*

*Le nouveau chef de guerre se présente pour son intronisation.*

Sabon sarki: Yakudima!

Le nouveau roi : Yakoudima !

Sabon sarki: Ya kamata yau da marece du a shaida ma mutane.

Le nouveau roi : Ce soir il faut informer toute la population.

Yakudima: Tau!

Yakoudima : D'accord !

Sabon sarki: Mai doki ya ma dokinshi sirdi da kaya

Le nouveau roi : Que tout celui qui a un cheval qu'il lui mette la selle.

Sabon sarki: Mu gewaye gari.

Le nouveau roi : Pour faire le tour de la ville.

Fadawa: Allah baka nasara!

Les notables : Gloire à toi !

Sabon sarki: Du jama'a su san hankalinmu ya gamu.

Le nouveau roi : Que toute la population sache bien que nous sommes unis.

Fadawa: Lafiyasa!

Les notables : Paix à vous !

Sabon sarki: Sabada mu kashe tsegumi.

Le nouveau roi : C’est pour qu’on arrête les racontards.

Fadawa: Haka nan ne.

Les notables : C’est comme ça.

Sabon sarki: Don tsegumi ba abun kirki ba ne.

Le nouveau roi : Parceque la zizanie n’est pas une bonne chose.

Fadawa: Lafiyasa!

Les notables : Paix à vous !

Sabon sarki: Haka za a yi. Du kowa ya je ya shiryo.

Le nouveau roi : Nous ferons ainsi. Que chacun retourne chez lui pour se préparer.

Fadawa: Lafiya sa!

Les notables : Paix à vous !

Sarkin yaƙi (*Ya zaro takobinsa ya zo gaban sarki ya yi rantsuwa ko ya ci amanar sarki.)*: Sarki Salihi, idan ka sani ko yanzu ko da dare ko da marece, idan ka sani ko na hwasa billahillazi La’ilahu Illahuwa.

Le chef de guerre (*Son sabre à la main se présent devant le roi et jure de ne la le trahir.)* :
Roi Salifi, je le jure si tu me donnes des ordres soit maintenant, la nuit ou le soir, si tu me le demandes et que je refuse d’obéir, je le jure.

*Sarki da mainawa ƴan uwansa da sauran jama’arsa kowa ya shirya suka yi hawan daba suna zagayen gari don su nuna wa mutane sun haɗe kansu. Makaɗa suna ta kiɗe-kiɗe da bushe-bushe. Mata suna ta buɗa. Sarkin yaƙi ma ba a bar shi baya ba, yazo da mutanensa saman dawakai kowa ya shirya da kyau.*

*Le roi, ses frères et les autres notables chacun sur son cheval font le tour de la ville pour montrer aux gens qu’ils sont unis. Les griots et les crieuses aminent la cérémonie.*

*Le chef de guerre avec ses gens arrivent sur des chevaux, bien harnachés.*



**Biographie**

An aifi malama Saude a birnin Maradi inda ta yi piramari da sakandari. Ta yi makarantar horon malamman ƙananan makarantu ta Tawa. Bayan ta yi shekara goma sha biyar tana koyarwa a cikin ƙananan makarantu ta ci gaba da karatunta a jami’ar Abdu Mummuni a fannin kimiyar harsuna. A yanzu tana aiki a Ministan Ƙananan Makarantu da Yaƙi da Jahilci, da Bunƙasa

Harsunan Ƙasa da Horo kan Ƴan ƙasanci, masammam ma a ma 'aikata mai kula da usalar koyarwa da bunƙasa harsunan ƙasa.

Madame Saoudé est née le 12 Novembre 1967 à Maradi où elle a fait ses études primaires et secondaires. Après l'obtention de son BEPC, elle a été orientée à l'école normale Kaocen de Tahoua où elle a suivi la formation des enseignants. Après quinze ans d'enseignement elle a fait un examen (spécial A), qui lui a permis de suivre ses études à l'université Abdou Moumouni de Niamey dans le domaine de la linguistique. Présentement elle est agent à la Direction des Curricula et de la Promotion des Langues Nationales au Ministère de l'Enseignement Primaire de l'Alphabétisation, de la Promotion des Langues Nationales et de l'Education Civique.